
MUSULUNCI
ISLAM
DA
AND
SUFANCI
SUFISM
A
IN
IFRIQIYYA
AFRICA
BLDR. IBRAHIM MUHAMMAD DANKYAURI
HAUSA

Intentionally left blank

ABUBUWAN DA KE CIKI

1) Matashiya.....4

2) Gabatarwa.....5

3) Addinin Musulunci.....7

4) Addinin Sufanci.....56

5) Sakamakon abinda Sufanci ya haifar a tsakanin Musulmai.....83

5) Ina muka dosa?.....84

1. MATASHIYA.

Da sunan Allah (nake farawa). Dukkan Yabo da Godiya sun tabbata ga Allah Ubangijin kowa da komai. Kuma dukkan Tsarkin da babu wani ɗatti tattare da shi, ya daɗa Tabbata ga Allah SWT. Babu Tsimi babu Dabara sai daga Allah AWJ. Ya Allah, Mai Rahama Mai jin ƙai, Ka ƙara daɗin Tsira da Aminci ga Bawanka kuma ManzonKa Annabin Rahama, Annabi Muhammad SAW, da Iyalan gidansa Tsarkaka da Sahabbansa Adalai da ragowar Salihan bayinKa waɗanda ke kan TafarkinKa Madaidaici, Tafarkin waɗanda Ka yi Ni'ima a garesu, ba tafarkin waɗanda Ka yi fushi da su ba, kuma ba tafarkin ɓatattu ba.

Don Allah, ina mai roƙon duk wanda zai karanta wannan Littafi ya karanta da idon basira, ya fahimci abinda na rubutu bisa doron Shari'ar dake cikin Alƙur'ani da Sunnah. **Sannan ya yiwa kansa da Ni da sauran Musulmai Adalci.**

Idan kai haƙiƙa Musulmi ne, irin Musuluncin da Annabi Muhammad Sallallahu 'Alaihi Wasallama (SAW) ya zo da shi, to ba za kayi riƙon molonka a matsayin Addini ba, sai dai abinda ya tabbata cikin Alkur'ani da Sunnar Fiyayyen halitta Annabin mu Annabin Rahama, wadda ta tabbata cikin hadisan sa ingantattu kuma bisa fahimtar magabatan mu na ƙwarai, waɗanda suke kan tafarkin Manzo tun asali.

Saboda haka ina mai baka shawara kada kayi ƙiwar karanta wannan Littafi daga bango zuwa bango la'alla ka fa'idantu. Kuma dai ƙiwar zata haifar maka da rashin fahimtar rubutun gaba ɗayansa.

A matsayina na ɗalibin Ilimi, In nayi kuskure a fahimtar da Ni ta hanyar da ta dace domin gyarawa. Kuma na gode Allah Ya saka da AlkhairinSa.

2. GABATARWA.

Mu sani cewar Alƙur'ani, wanda shine Jigon Ginshiƙin Addinin Musulunci, ana fahimtarsa ne ta hanyar bayanan da Annabi (SAW) ya yi ga ayoyinsa, da kuma aikin Manzo domin koyar da ma'anoninsa a aikace ga Sahabbansa da Matansa. Waɗannan bayanai da aiki na Manzo, su ake cewa SUNNAH kuma sune waɗanda aka taskace cikin Hadisansa ingantattu waɗanda manyan malamai suka rubuto cikin littattafan hadisai. Koda yake akwai hadisan da ba ingantattu ba, kai hasalima, wasu ƙarya aka yiwa Annabi aka jingina masa. To duk da haka, Malaman Hadisi sun tsatstsefe sun tankaɗe sun tace duk wani Hadisi bara-gurbi sun yi bayani a kansa. Littattafan Hadisai Sahihai sune kamar, Sahih Bukhari, Sahih Muslim. Wasu littattafan Hadisan sun haɗa da Sunan Abu Dawud, Ibn Majah, Nasa'i, Tirmidhi, Musnad Ahmad bin Hanbal, Muwaɗɗa Malik da sauransu.

Allah Ya yi alƙawarin kare Alƙur'ani inda Ya ce:

إِنَّا نَحْنُ نَزَّلْنَا ٱلذِّكْرَ وَإِنَّا لَهُۥ لَحَٰفِظُونَ

FASSARA

Lalle Mũ ne, Muka saukar da Ambato (Alƙur'ãni), kuma lalle Mũ, haƙĩka, Mãsu kiyayẽwane gare shi. [Surah Al-Ḥijr: 9]

Wannan kiyayewa ko kariya ga Alƙur'ani, kariya ce ta gaba ɗaya tun daga Rubutunsa, Karatunsa da lafazin da ya dace, Haddace shi cikin ƙirazan Hafizai, Fahimtar Ma'anoninsa da kuma Aiki tare dayin Da'awa da su.

Idan wasu sun karantashi da lafazin da bai dace ba, ko sun yi masa gurguwar fahimta, ko sun ƙi yin aiki da shi, ba shi ke nuna Allah bai bashi kariya ba. A'a, a ɗaya ɓangaren kuma akwai waɗanda suke karantashi da irin lafazin da aka saukar da shi tun asali, akwai waɗanda suka fahimce shi

haƙiƙanin fahimtar da Annabi SAW ya ɗora Sahabbansa akai kuma suke aiki da shi. Alhamdu lillahi.

Yana daga cikin baiwa Alƙur'ani da fahimtarsa kariya, ta yadda Allah SWT Ya tayar ko Ya samar da zaƙaƙuran malamai wajen yiwa Hadisan Manzon Allah SAW hidima ta kiyaye SANADIN SU DA MATANIN SU. Ilimin Hadisi ya bunƙasa ta yadda aka rarrabe da: Hadisi Sahih, Hadisi Hasan, Hadisi Da'ifi, Hadisi Maudu'i da sauransu. A shara'ance ana aiki da Hadisi Sahih da Hasan ne. Amma ka ga Hadisi Da'ifi da Maudu'i ba'a aiki da su. Wasu da yawa ba su san wannan ba. Allah Ya sauwaƙe.

Mai karatu ya iya tambaya; idan hakane me yasa aka rubuto, ko aka bar Hadisan da suke Da'ifai da Maudu'ai cikin littattafan Hadisai ba'a share su ba? Amsar shine, domin Kare Amanar Ilimi. Yadda ka ji, ka bayar da shi haka, tare da ƙarin bayanansa. Wannan kuma ba ruɗu bane, sai dai kawai idan kaso ka ruɗar da kanka. Allah Ya kiyaye.

Saboda haka, wannan Littafi ya ƙunshi ɓangarori kamar haka:

1) <u>Addinin Musulunci</u>; Allah, Mala'ika Jibril, Alƙur'ani, Annabi Muhammad, Sahabbansa da Matansa, Musuluncin. Kammalawa kan Musulunci.

2) Addinin Sufanci; Ma'anar Sufiy da Sufanci, Asalin Sufanci, Ilimin Baɗini, Ginshiƙan Sufanci, Taƙaitacen Tarihin wasu Sufayen, Ƴankorensu, Kammalawa kan Sufanci.

3) <u>Sakamakon abinda Sufanci ya haifar a tsakanin Musulmai.</u>

4) <u>Ina muka dosa?</u>

Ina mai roƙon Haƙuri, ƙana'a da Taufiƙi daga Allah SWT.

3. ADDININ MUSULUNCI

Hanya ce ɗoɗar, miƙaƙƙiya ta bautawa Allah 'Azza Wa Jalla (AWJ) Shi kaɗai, bisa koyarwar Manzon Rahama, farin Jakada Muhammad SAW ɗan Abdullahi, wadda sakamakon wannan aikin shine samun Tsira da Ɗaukaka da Rabauta duniya da lahira. Addinin Musulunci yana da Allahn da Ya Shar'anta a yi shi. Haka yana da Mala'ikan da yake kawo wahayin shi. Haka akwai Wahayin (watau Alƙur'ani). Sai kuma Manzon da ake aikowa Wahayin tare da fashin baƙin Wahayin daga bakinsa SAW. Sai kuma Sahabbansa da Matansa waɗanda Annabi ya karantawa tare da yi musu fashin baƙin Alƙur'anin lafazan da 'amalan. Sai kuma mu ragowar al'ummarsa SAW.

Sahabbai ne suka rubuce Alƙur'ani da bayanansa, wadda Manzon Allah SAW ya faɗa musu ya koyar da su. Su kuma suka koyar da Tabi'ai, su kuma suka koyar da Tabi'ut Tabi'ina har zuwa kanmu a yau.

Idan kayi inkarin aikin Sahabbai ko maganganunsu, to kayi inkarin rubutun Alƙur'anin dake hannunka da bayanansa gaba ɗaya. Yin hakan, kana son ka rushe Musulunci gaba ɗayansa kenan, tun daga tushe. Wannan kuwa munafuntar Addinin Musulunci da Musulmai ne, saboda wata ɓoyayyiyar manufarka, da waɗanda suka ɗora ka akai. Allah Ya sauwaƙe kuma Ya karemu daga SHARRIN irinku.

3.1) Allah Jalla Jalaluhu (JJH) Wanda Ya saukar kuma Ya Shara'anta Addinin Musulunci.

Wannan Suna na Allah, da wannan lafazin na -ALLAH- yazo cikin Alƙur'ani sau dubu ɗaya da ɗari takwas da arba'in da biyu (1842). Shine Babban Sunan Mahaliccin mu Abin bautar mu. Duk ragowar Sunayen Allah suna komawa ne ga Siffanta wannan Sunan na Allah. Idan kace ArRahmaan kana Siffanta Allah ne da cewa Shi ne Mafi Rahama. ArRahiim Allah ne Mafi jin ƙai. Da sauransu.

To Shi wannan Allahn Shine Ya faɗi ko waye Shi a cikin Alƙur'ani Mai Tsarki:

فَٱعۡلَمۡ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا ٱللَّهُ

Ka sani cewar babu abin bautawa da cancanta sai Allah..... Suratu Muhammad aya ta 19

إِنَّنِيٓ أَنَا ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّآ أَنَا۠ فَٱعۡبُدۡنِي وَأَقِمِ ٱلصَّلَوٰةَ لِذِكۡرِيٓ

"Lalle, Nĩ, Ni ne Allah. Bãbu abin bautawa fãce Ni. Sai ka bauta Mini, kuma ka tsayar da salla dõmin tuna Ni." Suratu DH aya ta 14.

ٱللَّهُ ٱلَّذِي خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ وَأَنزَلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءً

"Allah ne wanda Ya halicci sammai da ƙasa kuma Ya saukar da ruwa daga sama....." Suratu Ibrahim aya ta 32.

{ وَمَا خَلَقۡتُ ٱلۡجِنَّ وَٱلۡإِنسَ إِلَّا لِيَعۡبُدُونِ }

"Kuma Ban halitta Aljannu da Mutãne ba sai dõmin su bauta Mini." Surah Adh-Dhāriyāt aya ta56

ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ٱلۡحَيُّ ٱلۡقَيُّومُۚ لَا تَأۡخُذُهُۥ سِنَةٞ وَلَا نَوۡمٞۚ لَّهُۥ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۗ مَن ذَا ٱلَّذِي يَشۡفَعُ عِندَهُۥٓ إِلَّا بِإِذۡنِهِۦۚ يَعۡلَمُ مَا بَيۡنَ أَيۡدِيهِمۡ وَمَا خَلۡفَهُمۡۖ وَلَا يُحِيطُونَ بِشَيۡءٖ مِّنۡ عِلۡمِهِۦٓ إِلَّا بِمَا شَآءَۚ وَسِعَ كُرۡسِيُّهُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَۖ وَلَا يَـُٔودُهُۥ حِفۡظُهُمَاۚ وَهُوَ ٱلۡعَلِيُّ ٱلۡعَظِيمُ

Allah, bãbu wani Ubangiji fãce Shi, Rãyayye, Mai tsayuwa da kõme, gyangyaɗi bã ya kãma Shi, kuma barci bã ya kãma Shi, Shi ne da abinda yake a cikin sammai da abinda yake a cikin ƙasa. Wane ne wanda yake yin cẽto a wurinSa, fãce da izninSa? Yana sanin abinda yake a gaba gare su da abinda yake a bãyansu. Kuma bã su kẽwayẽwa da kõme daga ilminSa, fãce da abinda Ya so. KursiyyunSa ya yalwaci sammai da ƙasa. Kuma tsare su

bã ya nauyayarSa. Kuma Shi ne Maɗaukaki, Mai Girma. [Surah Al-Baqarah: 255]

هُوَ ٱللَّهُ ٱلَّذِى لَآ إِلَـٰهَ إِلَّا هُوَۖ عَـٰلِمُ ٱلْغَيْبِ وَٱلشَّهَـٰدَةِۖ هُوَ ٱلرَّحْمَـٰنُ ٱلرَّحِيمُ

هُوَ ٱللَّهُ ٱلَّذِى لَآ إِلَـٰهَ إِلَّا هُوَ ٱلْمَلِكُ ٱلْقُدُّوسُ ٱلسَّلَـٰمُ ٱلْمُؤْمِنُ ٱلْمُهَيْمِنُ ٱلْعَزِيزُ ٱلْجَبَّارُ ٱلْمُتَكَبِّرُۚ سُبْحَـٰنَ ٱللَّهِ عَمَّا يُشْرِكُونَ

هُوَ ٱللَّهُ ٱلْخَـٰلِقُ ٱلْبَارِئُ ٱلْمُصَوِّرُۖ لَهُ ٱلْأَسْمَآءُ ٱلْحُسْنَىٰۚ يُسَبِّحُ لَهُۥ مَا فِى ٱلسَّمَـٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِۖ وَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ

(Wanda Ya saukar da Alƙur'ani) Shi ne Allah, wanda bãbu wani abin bautãwa fãce Shi Masanin fake da bayyane, Shĩ ne Mai Rahama, Mai jin ƙai.

Shĩ ne Allah, wanda bãbu abin bautãwa fãce shi, Mai mulki, Mai tsarki, Aminci, Mai amintarwa, Mai Tsarẽwa, Mabuwãyi, Mai tilastãwa Mai nuna isa, tsarki ya tabbata a gare Shi daga abinda suke yi na shirki da Shi.

Shĩ ne Allah, Mai halitta, Mai ginãwa, Mai sũrantãwa. Yanã da sũnãye mãsu kyau, abinda ke a cikin sammai da ƙasa sunã tsarkake Shi, kuma Shĩ ne Mabuwãyi, Mai Hikima. [Surah Al-Ḥashr: 22-24]

ٱللَّهُ ٱلَّذِى خَلَقَ ٱلسَّمَـٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ وَأَنزَلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءً فَأَخْرَجَ بِهِۦ مِنَ ٱلثَّمَرَٰتِ رِزْقًا لَّكُمْۖ وَسَخَّرَ لَكُمُ ٱلْفُلْكَ لِتَجْرِىَ فِى ٱلْبَحْرِ بِأَمْرِهِۦۖ وَسَخَّرَ لَكُمُ ٱلْأَنْهَـٰرَ

وَسَخَّرَ لَكُمُ ٱلشَّمْسَ وَٱلْقَمَرَ دَآئِبَيْنِۖ وَسَخَّرَ لَكُمُ ٱلَّيْلَ وَٱلنَّهَارَ

وَءَاتَىٰكُم مِّن كُلِّ مَا سَأَلْتُمُوهُۚ وَإِن تَعُدُّوا۟ نِعْمَتَ ٱللَّهِ لَا تُحْصُوهَآۗ إِنَّ ٱلْإِنسَـٰنَ لَظَلُومٌ كَفَّارٌ

Allah ne wanda Ya halicci sammai da ƙasa kuma Ya saukar da ruwa daga sama, sa'an nan Ya fitar game da shi, daga 'ya'yan itãce arziki dõminku kuma Ya hõrẽ jirgin ruwa dõmin ya yi gudu a cikin tẽku da umurninSa, kuma Ya hõrẽ muku kõguna.

Kuma Ya hõrẽ muku rãnã da watã sunã madawwama biyu, kuma Ya hõrẽ muku dare da wuni.

Kuma Ya bã ku dukkan abin da kuka rõƙe Shi kuma idan kun ƙidaya, ni'imar Allah bã zã ku lissafe ta ba. Lalle ne mutum, haƙĩƙa, mai yawan zãlunci ne, mai yawan kãfirci [Surah Ibrāhīm: 32 -34]

Waɗannan ayoyi suna nuni ga Tauhidin Uluhiyya, Rububiyya, da Sifaat da kuma Rahamar Allah da jin ƙai ga Talikai. Gurguwar fahimta ga duk wannan ya haifar da yawa daga cikin Musulmai, an ja su ga Shirka a cikin wannan ƙasa ta mu.

Allah Ya jiƙan Sheikh Ja'afar Mahmoud Adam Kano, Dr. Idris Abdul'Aziz Dutsen Tanshi Bauchi, Sheikh Muhammad Lawan Albanin Zariya, Dattijon arziki Sheikh Dr. Ibrahim Bamba BUK, Dattijon arziki Sheikh Dr. Abubakar Mahmoud Gumi. Da ragowar malamai wadanda suka rasu da na raye, masu kira kan TAUHIDI da SUNNAR Annabi. Domin shine babban GINSHIƘIN IBADA GA ALLAH. Idan babu TAUHIDI, dukkan IBADA ta Rushe. Allah Ya kiyaye.

مَا تَعۡبُدُونَ مِن دُونِهِۦٓ إِلَّآ أَسۡمَآءٗ سَمَّيۡتُمُوهَآ أَنتُمۡ وَءَابَآؤُكُم مَّآ أَنزَلَ ٱللَّهُ بِهَا مِن سُلۡطَٰنٍۚ إِنِ ٱلۡحُكۡمُ إِلَّا لِلَّهِۚ أَمَرَ أَلَّا تَعۡبُدُوٓاْ إِلَّآ إِيَّاهُۚ ذَٰلِكَ ٱلدِّينُ ٱلۡقَيِّمُ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعۡلَمُونَ

Ba ku bauta wa kõme, baicinSa, fãce waɗansu sũnãye waɗanda kuka ambace su, kũ da ubanninku. Allah bai saukar da wani dalĩli ba game da su. Bãbu hukunci fãce na Allah. Ya yi umurnin kada ku bauta wa kõwa fãce Shi. Wancan ne addini madaidaici, kuma amma mafi yawan mutãne ba su sani ba." [Surah Yūsuf: 40]

Tun da Allah Ya halicceka kuma kayi hankali, kake ganin rana da wata, yini da dare, ruwan sama mai kwararowa daga sama, tsirrai masu bunƙurowa daga ƙasa. Ba ka taɓa jin wani ko a mafarki cikin irinka ɗan Adam ko Aljani, ya ce shine yake waɗannan abubuwan ba. Sannan ka duba halittar ka da ni'imomin da Allah Ya yi maka. Ba ka taɓa jin wani yace shi yake baka damar cin abinci ko shan ruwa ko sarrafa zuciyarka wajen yin aikinta na tura

jini cikin dukkan sassan jikinka. Saboda haka, ina hankalinka yake da za'a jaka cikin bautawa wanin Allah, mai mutuwa mai ƙarewa kamarka? Tir da irin wannan hali - na shirka.

إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَغۡفِرُ أَن يُشۡرَكَ بِهِۦ وَيَغۡفِرُ مَا دُونَ ذَٰلِكَ لِمَن يَشَآءُۚ وَمَن يُشۡرِكۡ بِٱللَّهِ فَقَدِ ٱفۡتَرَىٰٓ إِثۡمًا عَظِيمًا

Lalle ne, Allah ba Ya gãfarta a yi shirki game da Shi, kuma Yana gãfarta abin da yake bãyan wannan ga wanda Yake so, kuma wanda ya yi shirki da Allah, to, lalle ne ya ƙirƙiri zunubi mai girma. [Surah An-Nisāʾ: 48]

إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَغۡفِرُ أَن يُشۡرَكَ بِهِۦ وَيَغۡفِرُ مَا دُونَ ذَٰلِكَ لِمَن يَشَآءُۚ وَمَن يُشۡرِكۡ بِٱللَّهِ فَقَدۡ ضَلَّ ضَلَٰلَۢا بَعِيدًا

Lalle ne, Allah ba Ya gãfarta a yi shirka da Shi, kuma Yana gãfarta abinda yake bãyan wannan, ga wanda Yake so. Kuma wanda ya yi shirka da Allah, to, lalle ne ya ɓace ɓata mai nĩsa. [Surah An-Nisāʾ: 116]

Saboda haka, Allah SWT kawai ake bautawa. Shike bada Umarni da Hani abi. GareShi ake roƙon arziki, haihuwa, lafiya, ruwan sama, agajin gaggawa, da sauransu. GareShi ake fatan Rahama da jinƙai, ake tsoron AzabarSa da FushinSa. GareShi ake Tsarkake Ibada Shi kaɗai, SWT, ake Sujada, Ruku'u, Zikri da sauransu. Idan kayi duk wannan cikin sani ga wani ba Allah ba, to ka zama Mushrik, Kafiri, Zindiƙi.

Ga masu kiran wanin Allah ku saurara:

وَمَنۡ أَضَلُّ مِمَّن يَدۡعُواْ مِن دُونِ ٱللَّهِ مَن لَّا يَسۡتَجِيبُ لَهُۥٓ إِلَىٰ يَوۡمِ ٱلۡقِيَٰمَةِ وَهُمۡ عَن دُعَآئِهِمۡ غَٰفِلُونَ

Kuma wãne ne mafi ɓata daga wanda ke kiran wanin Allah wanda bã zai karɓa masa ba, har Rãnar Kiyama, alhãli sũ (waɗanda ake kiran) shagaltattu ne daga kiransu? [Surah Al-Aḥqāf: 5]

يُولِجُ ٱلَّيۡلَ فِي ٱلنَّهَارِ وَيُولِجُ ٱلنَّهَارَ فِي ٱلَّيۡلِ وَسَخَّرَ ٱلشَّمۡسَ وَٱلۡقَمَرَۖ كُلٌّ يَجۡرِي لِأَجَلٖ مُّسَمًّىۚ ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبُّكُمۡ لَهُ ٱلۡمُلۡكُۚ وَٱلَّذِينَ تَدۡعُونَ مِن دُونِهِۦ مَا يَمۡلِكُونَ مِن قِطۡمِيرٍ

إِن تَدۡعُوهُمۡ لَا يَسۡمَعُواْ دُعَآءَكُمۡ وَلَوۡ سَمِعُواْ مَا ٱسۡتَجَابُواْ لَكُمۡۖ وَيَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ يَكۡفُرُونَ بِشِرۡكِكُمۡۚ وَلَا يُنَبِّئُكَ مِثۡلُ خَبِيرِۢ

Yanã shigar da dare a cikin yini, kuma Yanã shigar da yini a cikin dare. Kuma Ya hõre rãnã da watã kõwannensu yanã gudãna zuwa ga ajali ambatacce. Wannan Shĩ ne Allah, Ubangijinku, gare Shi mulki yake, kuma waɗanda kuke kira waninSa bã su mallakar kõ fãtar gurtsun dabĩno (wadda ta lullube kwallon dan dabino).

Idan kun kira su, bã zã su ji kiranku ba, kuma kõ sun jiya, bã zã su karɓa muku ba, kuma a Rãnar Kiyama zã su kãfirce wa shirkinku, kuma bãbu mai bã ka lãbãri, kamar wanda ya sani. [Surah Fāṭir: 13-14]

3.2) Mala’ikun Allah:

Wannan suna na Mala'ika da wannan lafazi kawai na -MALA'IK- ya zo sau saba'in da uku (73) a cikin Alkur'ani mai Tsarki. Mala'iku Halittun Allah ne kuma bayinSa ne, waɗanda Ya halitta su domin kawai su bauta masa, ba tare da Ya basu zaɓi kamar yadda Ya baiwa ɗan Adam ba. Su ba sa saɓawa Allah ko kaɗan. Kuma ba mataimakan Allah ba ne, domin Allah Ya wadatu da komai. Su kuma ba yayan Allah ba ne. Hujja kan haka shine faɗin Allah SWT cikin Alƙur’ani mai Tsarki:

بسم الله الرحمان الرحيم

ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ فَاطِرِ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ جَاعِلِ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةِ رُسُلًا أُوْلِيٓ أَجۡنِحَةٖ مَّثۡنَىٰ وَثُلَٰثَ وَرُبَٰعَۚ يَزِيدُ فِي ٱلۡخَلۡقِ مَا يَشَآءُۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ

Gõdiya ta tabbata ga Allah, Mai fãra (Ya ƙago, ba tare da ya kwaikwaiya gurin wani ba) halittar sammai da ƙasã, Mai sanya malã'iku manzanni mãsu fukãfukai, bibbiyu, da uku-uku da hurhuɗu. Yanã ƙãrãwar abin da Ya ke so a cikin halittar. Lalle Allah Mai ĩkon yi ne a kan kõme. [Surah Fāṭir: 1]

لَّن يَسْتَنكِفَ ٱلْمَسِيحُ أَن يَكُونَ عَبْدًا لِّلَّهِ وَلَا ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ ٱلْمُقَرَّبُونَ ۚ وَمَن يَسْتَنكِفْ عَنْ عِبَادَتِهِۦ وَيَسْتَكْبِرْ فَسَيَحْشُرُهُمْ إِلَيْهِ جَمِيعًا

Masĩhu (Isa ɗan Maryam) bã ya ƙyãmar ya kasance bãwa ga Allah, kuma haka malã'ikun nan makusanta. Kuma wanda ya yi ƙyãmar bautarSa kuma ya yi girman kai, to, zai tãra su zuwa gare shi gabã ɗaya. [Surah An-Nisāʾ: 172]

يُنَزِّلُ ٱلْمَلَٰٓئِكَةَ بِٱلرُّوحِ مِنْ أَمْرِهِۦ عَلَىٰ مَن يَشَآءُ مِنْ عِبَادِهِۦٓ أَنْ أَنذِرُوٓا۟ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّآ أَنَا۠ فَٱتَّقُونِ

Yanã sassaukar da malã'iku da Rũhi (Mala'ika Jibril AS) daga umurninSa a kan wanda Yake so daga bãyinSa, cẽwa ku yi gargaɗĩ cẽwa: Lalle ne shĩ, bãbu abin bautãwa fãce Ni (Allah), sabõda haka ku bĩ Ni (Allahu) da taƙawa. [Surah An-Naḥl: 2]

ٱللَّهُ يَصْطَفِى مِنَ ٱلْمَلَٰٓئِكَةِ رُسُلًا وَمِنَ ٱلنَّاسِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ سَمِيعٌۢ بَصِيرٌ

Allah nã zãɓen Manzanni daga Malã'iku kuma daga Mutãne. Lalle Allah, Mai ji ne, Mai gani. [Surah Al-Ḥajj: 75]

إِن كُلُّ مَن فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ إِلَّآ ءَاتِى ٱلرَّحْمَٰنِ عَبْدًا

Dukkan wanda yake a cikin sammai da ƙasa bai zama ba fãce mai jẽ wa Mai Rahama ne yanã bãwã. [Surah Maryam: 93]

3.3 Alƙur'ani mai Tsarki: da Allah Ya saukarwa Annabi (SAW) ta hanyar Mala'ika Jibril AS:

Alƙur'ani da wannan lafazin ya zo sau hamsin (50) cikin Alƙur'ani. Sannan ya zo da wasu lafuzan kamar AlFurqan, AlKitaab, AzZikr da sauransu. Shine jigon kundin Musulunci gaba ɗayansa. Duk wani bayani ko aikin Manzo cikin Addini, yana komawa ne ga fassara da fashin baƙi kan Alƙur'ani. Wanda ya tozarta shi (Alƙur'anin), ya tozarta Addinin Musulunci da Allah da ManzonSa da Musulmi baki ɗaya. Wanda ya so shi, ya fahimce shi, ya yi aiki da shi, ya so Allah da ManzonSa da Musulmai baki ɗaya.

بسم الله الرحمان الرحيم

الٓمٓ
ذَٰلِكَ ٱلۡكِتَٰبُ لَا رَيۡبَۛ فِيهِۛ هُدٗى لِّلۡمُتَّقِينَ

Alif, Lām, Meem.
Wãncan ne Littãfi (Alƙur'ani), bãbu shakka a cikinsa, shiriya ne ga mãsu taƙawa (masu kiyaye dokokin Allah da ikhlasi). Surah Al-Baqarah: 1-2

وَإِنَّهُۥ لَتَنزِيلُ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ
نَزَلَ بِهِ ٱلرُّوحُ ٱلۡأَمِينُ
عَلَىٰ قَلۡبِكَ لِتَكُونَ مِنَ ٱلۡمُنذِرِينَ
بِلِسَانٍ عَرَبِيّٖ مُّبِينٖ
وَإِنَّهُۥ لَفِي زُبُرِ ٱلۡأَوَّلِينَ

Kuma lalle shi (Alƙur'ãni), haƙĩƙa, saukarwar Ubangijin halittu ne.
Rũhi (Mala'ika Jibril) amintacce ne ya sauka da shi.
A kan zũciyarka (Ya Muhammad), dõmin ka kasance daga mãsu gargaɗi.
Da harshe na Larabci mai bayãni.

Kuma lalle shi, haƙĩƙa, yanã a cikin littattafan (Manzannin) farko. [Surah Ash-Shuʿarāʾ: 192-196].

إِنَّا نَحۡنُ نَزَّلۡنَا ٱلذِّكۡرَ وَإِنَّا لَهُۥ لَحَٰفِظُونَ

Lalle Mũ ne, Muka saukar da Ambato (Alƙur'ãni), kuma lale Mũ, haƙĩƙa, Mãsu kiyayẽwa ne gare shi. [Surah Al-Ḥijr: 9]

Duk wadanda ayoyi, suna nuni ga cewar lallai Alƙur'ani gaba ɗayansa saukakke ne daga Allah Ubangijin Talikai ta hannun Mala'ika Jibril AS Amintaccen Allah, zuwa ga wani Manzon, Amintaccen Allah - Annabi Muhammad SAW.

Shin a yau, ga Musulmai akwai wani Saukakken Umarni da Hani baicin Alƙur'ani? Babu, da fadinSa Rabbul 'Izzati;

حُرِّمَتۡ عَلَيۡكُمُ ٱلۡمَيۡتَةُ وَٱلدَّمُ وَلَحۡمُ ٱلۡخِنزِيرِ وَمَآ أُهِلَّ لِغَيۡرِ ٱللَّهِ بِهِۦ وَٱلۡمُنۡخَنِقَةُ وَٱلۡمَوۡقُوذَةُ وَٱلۡمُتَرَدِّيَةُ وَٱلنَّطِيحَةُ وَمَآ أَكَلَ ٱلسَّبُعُ إِلَّا مَا ذَكَّيۡتُمۡ وَمَا ذُبِحَ عَلَى ٱلنُّصُبِ وَأَن تَسۡتَقۡسِمُواْ بِٱلۡأَزۡلَٰمِۚ ذَٰلِكُمۡ فِسۡقٌۗ ٱلۡيَوۡمَ يَئِسَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِن دِينِكُمۡ فَلَا تَخۡشَوۡهُمۡ وَٱخۡشَوۡنِۚ ٱلۡيَوۡمَ أَكۡمَلۡتُ لَكُمۡ دِينَكُمۡ وَأَتۡمَمۡتُ عَلَيۡكُمۡ نِعۡمَتِي وَرَضِيتُ لَكُمُ ٱلۡإِسۡلَٰمَ دِينٗاۚ فَمَنِ ٱضۡطُرَّ فِي مَخۡمَصَةٍ غَيۡرَ مُتَجَانِفٖ لِّإِثۡمٖ فَإِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٞ

An haramta muku mũshe da jini da nãman alade da abin da aka ambaci sũnan wanin Allah a gare shi, da mãƙararriya da jefaffiya da mai gangarõwa da sõkakkiya, da abin da mãsu dãgi (dabbobi masu farauta) suka ci, fãce abin da kuka yanka, da abin da aka yanka a kan gunki (shĩ ma an haramta). Kuma kada ku yi rabo (canki-canka) da kibiyoyi na cãca wannan fãsiƙanci ne, A yau wadanda suka kãfirta sun yanke ƙauna daga addininku. Sabõda haka kada ku ji tsõronsu kuma ku ji tsõroNa. **A yau Nã kammalã muku addininku, Kuma Nã cika ni'imaTa a kanku, Kuma Nã yarda da Musulunci ya zama addini a gare ku.** To, wanda aka sanya wa lalũra a

cikin yunwa mai tsanani, bã yana mai karkata zuwa ga wani zunubi ba, to, lalle ne Allah Mai gãfara ne, Mai jin ƙai. [Surah Al-Māʾidah: 3]

Saboda haka, abinda da bai zama Addini ba lokacin Manzo da Sahabbansa, to komai kyansa da duk abinda aka jingina masa na falala a yau, ba zai taɓa zama Addina ba. An riga an gama, an ɗage alƙalami kuma takardu sun bushe, da faɗinSa Zal-Jalali wal'Ikraami: {al-yauma akmaltu lakum dinakum}.

Samun wasu zindiƙai suce sun yi mafarki an basu wani nau'i na ibada kamar salatul fatih, ƙarya ce tsagwaronta, kuma zargin Fiyayyen Halitta ne da ɓoye wani abu ga Sahabbansa na Wahayi, har sai bayan shekaru sama da dubu sannan wai ya baiwa wani zindiƙi!

Tun kafin Annabi SAW yayi wafati (ya mutu), Allah SWT Ya ja kunnensa da faɗinSa cewa;

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلرَّسُولُ بَلِّغۡ مَآ أُنزِلَ إِلَيۡكَ مِن رَّبِّكَۖ وَإِن لَّمۡ تَفۡعَلۡ فَمَا بَلَّغۡتَ رِسَالَتَهُۥۚ وَٱللَّهُ يَعۡصِمُكَ مِنَ ٱلنَّاسِۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهۡدِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلۡكَٰفِرِينَ

Yã kai Manzo! Ka iyar da abinda aka saukar zuwa gare ka daga Ubangijinka. Kuma idan ba ka aikata ba, to, ba ka iyar da manzancinSa ba ke nan. Kuma Allah Yanã tsare ka daga mutãne. Lalle ne, Allah bã Ya shiryar da mutãne kãfirai. [Surah Al-Māʾidah: 67]

3.4 Manzon Allah: Annabi Muhammad SAW

Tun kafin a haifi Manzon Allah SAW, Allah SWT Ya bayar da labarin zuwansa a cikin Littattafan da Allah Ya saukarwa Manzannin da suka gabace shi. Haka Sahabbansa masu daraja, suma Allah AWJ Ya bayar da labarin su da kuma siffarsu cikin Linjila da Attaura.

وَإِذۡ قَالَ عِيسَى ٱبۡنُ مَرۡيَمَ يَٰبَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ إِنِّي رَسُولُ ٱللَّهِ إِلَيۡكُم مُّصَدِّقٗا لِّمَا بَيۡنَ يَدَيَّ مِنَ ٱلتَّوۡرَىٰةِ وَمُبَشِّرَۢا بِرَسُولٖ يَأۡتِي مِنۢ بَعۡدِي ٱسۡمُهُۥٓ أَحۡمَدُۖ فَلَمَّا جَآءَهُم بِٱلۡبَيِّنَٰتِ قَالُواْ هَٰذَا سِحۡرٞ مُّبِينٞ

"Kuma a lõkacin da Ĩsã ɗan Maryama ya ce: "Yã Banĩlsrã'ĩla! Lalle nĩ Manzon Allah ne zuwa gare ku, mai gaskata abin da ke gaba gare ni na Attaura, kuma mai bãyar da bushãra da wani Manzo da ke zuwa a bãyãna, Sũnansa Ahmad (Mashãyabo)." To, a lõkacin da ya jẽ musu da hujjõji, suka ce: "Wannan sihiri ne, bayyananne." [Surah Aṣ-Ṣaff: 6]

Sunan Manzon Allah SAW da lafazin -Muhammad- ya zo cikin Alƙur'ani mai Tsarki sau 4. Amma Allah Ya ambace shi da sunaye cikin Alƙur'ani kamar haka; Ahmad, Rasul, Nabiy, Mudassir, Muzammil, da sauransu.

Annabi Muhammad SAW, yana cikin bayin Allah na gari matuƙa. Mutum ne, ba Aljani ba, ba kuma Mala'ika ba. Bai san gaibu ba sai abinda Allah SWT Ya sanarda shi. Haka ba shi ke arzuta kanshi da kanshi ba, face abinda Sallah SWT Ya ƙaddara masa na rayuwarsa. Sannan a matsayinsa na mutum, yana rashin lafiya, yana jin yunwa, yana cin abinci da biyan bukata na bayan gida, yana bacci, yana yin aure har da yaya mata da maza SAW. Sai dai shi, bayan Allah Ya ba shi Manzanci, to Ya kuma fifita shi kan ragowar halittu da abubuwa masu yawa.

{..... ٱللَّهُ أَعۡلَمُ حَيۡثُ يَجۡعَلُ رِسَالَتَهُۥۗ .....}

"..... Allah Mafi sanin inda Yake sanya manzancinSa ne....."
[Surah Al-Anʿām: 124]

Yadda Allah SWT Ya zaɓe shi da Manzanci kuma Ya ba shi Hali mafi kyau, kamar haka ne Allah Ya zaɓa masa Sahabbai da Mata mafi zama na gari da halaiya mafi kyau akan ragowar al'umma.

Duk da haka yana nan kan matsayin sa na mutum kuma bawa amma Manzo, mai bautar Allah kamar ragowar bayin Allah da Manzannin Allah. Fifita shi

da Allah Ya yi, ba shi ke nufin kuma a ɗauki Siffar Allah ko aikin Allah, a dangana masa ba. Yin hakan Shirka ne. Ka yarda ko kar ka yarda wannan kai ta shafa. Kasancewarsa mutum shi yasa Allah SWT Ya ce shi SAW mai mutuwa ne kamar ragowar mutane.

إِنَّكَ مَيِّتٌ وَإِنَّهُم مَّيِّتُونَ

Lalle kai (Ya RasululLah) mai mutuwa ne, kuma su mã lalle mãsu mutuwa ne. [Surah Az-Zumar: 30].

Tabbas Manzon Allah SAW ya rayu a duniya kuma ya rasu ya koma ga Mahaliccinsa, kamar yadda ragowar Annabawa da Manzanni suka rasu suka koma ga Mahaliccinsu gabaninsa. Allah SWT Ya yi daɗin salati da aminci garesu baki ɗaya.

Manzon Allah SAW tsarkakakke ne daga Ubangijinsa kamar yadda yazo cikin Alƙur'ani mai Tsarki. Ba shi bukatar a ƙirƙiri ƙarya a jingina masa wai don nuna Karamarsa ko Mu'ujizarsa. Alƙur'ani da Hadisansa ingantattu sun wadatar.

Manzon Allah SAW shine mutum ɗaya tilo wadda indai kai Musulmi ne dole ka so shi fiye da kowa a doron ƙasarnan. Dole ka so shi, ka yi masa ɗa'a cikin duk abinda ya umarce ka, ko ya hanaka. Daga son Allah sai na Manzo sai na Mahaifa idan suna kan Tafarkin Manzo sai ragowar salihan bayin Allah na gari waɗanda suka yi riƙo da KITABU da SUNNAH, ba waɗanda suka ƙirƙirowa kansu ɗariƙun shirka da sharholiya ba.

Allah Ya sani cewar a cikin zamani, za a samu masu yiwa Annabi ƙarya, da masu zagin Sahabbansa da Matansa, da masu faɗa da Sunnarsa, Kai har da masu da'awar Annabta da ma Allantaka.

Shi ya sanya Allah SWT Ya ja kunnen al'umma cikin Alƙur'ani, haka Manzon Allah SAW cikin hadisansa ingantattu.

Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce:

مَّا كَانَ مُحَمَّدٌ أَبَآ أَحَدٍ مِّن رِّجَالِكُمْ وَلَٰكِن رَّسُولَ ٱللَّهِ وَخَاتَمَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ ۗ وَكَانَ ٱللَّهُ بِكُلِّ شَىْءٍ عَلِيمًا

Muhammadu bai kasance uban kõwa ba daga mazanku, kuma amma shĩ yã kasance Manzon Allah kuma cikon Annabãwa. Kuma Allah Ya kasance Masani ga kõme. [Surah Al-Aḥzāb: 40]

وَمَا مُحَمَّدٌ إِلَّا رَسُولٌ قَدْ خَلَتْ مِن قَبْلِهِ ٱلرُّسُلُ ۚ أَفَإِيْن مَّاتَ أَوْ قُتِلَ ٱنقَلَبْتُمْ عَلَىٰٓ أَعْقَٰبِكُمْ ۚ وَمَن يَنقَلِبْ عَلَىٰ عَقِبَيْهِ فَلَن يَضُرَّ ٱللَّهَ شَيْـًٔا ۗ وَسَيَجْزِى ٱللَّهُ ٱلشَّٰكِرِينَ

Kuma Muhammadu bai zama ba face manzo lalle ne manzanni sun shũɗe a gabãninsa. Ashe idan ya mutu ko kuwa aka kashe shi, zã kujũya a kan dugaduganku? To, wanda ya jũya a kan dugadugansa, bã zai cũci Allah da kõme ba. Kuma Allah zai sãka wa mãsu gõdiya. [Surah Āli-ʿImrān: 144]

مُّحَمَّدٌ رَّسُولُ ٱللَّهِ ۚ وَٱلَّذِينَ مَعَهُۥٓ أَشِدَّآءُ عَلَى ٱلْكُفَّارِ رُحَمَآءُ بَيْنَهُمْ ۖ تَرَىٰهُمْ رُكَّعًا سُجَّدًا يَبْتَغُونَ فَضْلًا مِّنَ ٱللَّهِ وَرِضْوَٰنًا ۖ سِيمَاهُمْ فِى وُجُوهِهِم مِّنْ أَثَرِ ٱلسُّجُودِ ۚ ذَٰلِكَ مَثَلُهُمْ فِى ٱلتَّوْرَىٰةِ ۚ وَمَثَلُهُمْ فِى ٱلْإِنجِيلِ كَزَرْعٍ أَخْرَجَ شَطْـَٔهُۥ فَـَٔازَرَهُۥ فَٱسْتَغْلَظَ فَٱسْتَوَىٰ عَلَىٰ سُوقِهِۦ يُعْجِبُ ٱلزُّرَّاعَ لِيَغِيظَ بِهِمُ ٱلْكُفَّارَ ۗ وَعَدَ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ مِنْهُم مَّغْفِرَةً وَأَجْرًا عَظِيمًا

Muhammadu Manzon Allah ne. Kuma waɗannan da ke tãre da shi (Sahabbansa) mãsu tsanani ne a kan kãfirai, mãsu rahama ne a tsakãninsu, kanã ganin su sunã mãsu rukũ'i mãsu sujada, sunã nẽman falala daga Ubangijinsu, da yardarSa. Alãmarsu tanã a cikin fuskõkinsu, daga kufan sujuda. Wannan shĩ ne siffarsu a cikin Attaura. Kuma siffarsu, a cikin Injĩla ita ce kamar tsiron shũka wanda ya fitar da rẽshensa, sa'an nan ya ƙarfafa shi, ya yi kauri, sa'an nan ya daidaita a kan ƙafãfunsa, yanã bãyar da sha'awa ga mãsu shũkar' dõmin (Allah) Ya fusãtar da kãfirai game da su. Kuma Allah Ya yi wa'adi ga waɗanda suka yi ĩmãni, kuma suka aikata ayyukan ƙwarai, daga cikinsu, da gãfara da ijãra (lada) mai girma. [Surah Al-Fatḥ: 29].

قُلۡ إِنَّمَآ أَنَا۠ بَشَرٞ مِّثۡلُكُمۡ يُوحَىٰٓ إِلَيَّ أَنَّمَآ إِلَٰهُكُمۡ إِلَٰهٞ وَٰحِدٞۖ فَمَن كَانَ يَرۡجُواْ لِقَآءَ رَبِّهِۦ فَلۡيَعۡمَلۡ عَمَلٗا صَٰلِحٗا وَلَا يُشۡرِكۡ بِعِبَادَةِ رَبِّهِۦٓ أَحَدَۢا

Ka ce: "Nĩ, mutum ne kawai kamarku, anã yin wahayi zuwa gare ni cewa: Lalle ne, Abin bautawarku, Abin bautawa Guda ne, sabõda haka wanda ya kasance yanã fãtan haɗuwa da Ubangijinsa, to, sai ya yi aiki na ƙwarai. Kuma kada ya haɗa kõwa ga bauta wa Ubangijinsa." [Surah Al-Kahf: 110]

وَمَآ أَرۡسَلۡنَا مِن قَبۡلِكَ إِلَّا رِجَالٗا نُّوحِيٓ إِلَيۡهِمۡۖ فَسۡـَٔلُوٓاْ أَهۡلَ ٱلذِّكۡرِ إِن كُنتُمۡ لَا تَعۡلَمُونَ

بِٱلۡبَيِّنَٰتِ وَٱلزُّبُرِۗ وَأَنزَلۡنَآ إِلَيۡكَ ٱلذِّكۡرَ لِتُبَيِّنَ لِلنَّاسِ مَا نُزِّلَ إِلَيۡهِمۡ وَلَعَلَّهُمۡ يَتَفَكَّرُونَ

Kuma ba Mu aika daga gabaninka ba (Ya Rasulullah), fãce waɗansu mazãje Muna yin wahayi zuwa gare su. Sai ku tambayi mutãnen Ambato idan kun kasance ba ku sani ba.

Da hujjõji bayyanannu da littattafai kuma Mun saukar da Ambato (Alƙur'ani) zuwa gare ka (Ya Muhammad), dõmin ka bayyanawa mutãne abin da aka sassaukar zuwa gare su, kuma don ɗammãnin su, su yi tunãni. [Surah An-Naḥl: 43-44]

هُوَ ٱلَّذِي بَعَثَ فِي ٱلۡأُمِّيِّـۧنَ رَسُولٗا مِّنۡهُمۡ يَتۡلُواْ عَلَيۡهِمۡ ءَايَٰتِهِۦ وَيُزَكِّيهِمۡ وَيُعَلِّمُهُمُ ٱلۡكِتَٰبَ وَٱلۡحِكۡمَةَ وَإِن كَانُواْ مِن قَبۡلُ لَفِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٖ

Shĩ ne wanda Ya aika, a cikin mabiya al'ãdu (Larabawa), wani Manzo (Annabi Muhammad SAW) daga gare su yanã karanta ãyõyin Sa a kansu, kuma yanã tsarkake su, kuma yanã sanar da su littafin (Alƙur'ani) da hikimarsa (Sunnah) kõ da yake sun kasance daga gabãninsa lalle sunã a cikin ɓata bayyanãnna. [Surah Al-Jumuʿah: 2]

وَمَا صَاحِبُكُم بِمَجۡنُونٖ

Kuma abokinku ba mahaukaci ba ne. [Surah At-Takwīr: 22]

نٓ وَٱلۡقَلَمِ وَمَا يَسۡطُرُونَ
مَآ أَنتَ بِنِعۡمَةِ رَبِّكَ بِمَجۡنُونٖ
وَإِنَّ لَكَ لَأَجۡرًا غَيۡرَ مَمۡنُونٖ
وَإِنَّكَ لَعَلَىٰ خُلُقٍ عَظِيمٖ

Ñ. Na rantse da alƙalami da abin da (marubũta) suke rubũtãwa.
Kai, sabõda ni'imar Ubangijinka, bã mahaukaci kake ba.
Kuma, lalle, haƙĩƙa kanã da lãdar da bã ta yankewa.
Kuma, lalle haƙiƙa kana a kan hãlãyen kirki, manya. [Surah Al-Qalam: 1-4]

قُل لَّآ أَقُولُ لَكُمۡ عِندِي خَزَآئِنُ ٱللَّهِ وَلَآ أَعۡلَمُ ٱلۡغَيۡبَ وَلَآ أَقُولُ لَكُمۡ إِنِّي مَلَكٌۖ إِنۡ أَتَّبِعُ إِلَّا مَا يُوحَىٰٓ إِلَيَّۚ قُلۡ هَلۡ يَسۡتَوِي ٱلۡأَعۡمَىٰ وَٱلۡبَصِيرُۚ أَفَلَا تَتَفَكَّرُونَ

Ka ce: "Ba zan ce muku, a wurina akwai taskõkin Allah ba. Kuma ba ni sanin gaibi, kuma ba ni gaya muku cẽwa ni malã'ika ne. Ba ni bi, fãce abin da ake yiwo wahayi zuwa gare ni." Ka ce: "Shin, makãho da mai gani sunã daidaita? Shin fa, ba ku yin tunãni?" [Surah Al-Anʿām: 50]

قُل لَّآ أَمۡلِكُ لِنَفۡسِي ضَرّٗا وَلَا نَفۡعًا إِلَّا مَا شَآءَ ٱللَّهُۗ لِكُلِّ أُمَّةٍ أَجَلٌۚ إِذَا جَآءَ أَجَلُهُمۡ فَلَا يَسۡتَـٔۡخِرُونَ سَاعَةٗ وَلَا يَسۡتَقۡدِمُونَ

Ka ce: "Ba na mallaka wa kaina wata cũta, haka kuma wani amfãni, sai abin da Allah Ya so. Ga kõwace al'umma akwai ajali, idan ajalinsu ya zo, to, bã zã su yi jinkiri daga gare shi ba, kõ dã sã'ã guda, kuma bã zã su gabãta ba." [Surah Yūnus: 49]

مَّآ أَفَآءَ ٱللَّهُ عَلَىٰ رَسُولِهِۦ مِنۡ أَهۡلِ ٱلۡقُرَىٰ فَلِلَّهِ وَلِلرَّسُولِ وَلِذِي ٱلۡقُرۡبَىٰ وَٱلۡيَتَٰمَىٰ وَٱلۡمَسَٰكِينِ وَٱبۡنِ ٱلسَّبِيلِ كَيۡ لَا يَكُونَ دُولَةَۢ بَيۡنَ ٱلۡأَغۡنِيَآءِ مِنكُمۡۚ وَمَآ ءَاتَىٰكُمُ ٱلرَّسُولُ فَخُذُوهُ وَمَا نَهَىٰكُمۡ عَنۡهُ فَٱنتَهُواْۚ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَۖ إِنَّ ٱللَّهَ شَدِيدُ ٱلۡعِقَابِ

Abin da Allah Ya sanya shi ganĩma ga Manzon Sa dagamutãnen ƙauyukan nan, to, na Allah ne, kuma na Manzon Sa ne kuma na mãsu dangantaka da mãrayu da miskĩnai da ɗan hanya* (matafiyi) ne dõmin kada ya kasance abin shãwãgi a tsakãnin mawadãta daga cikinku kuma abin da Manzo ya bã ku, to, ku kama shi, kuma abin da ya hane ku, to, ku bar shi. Kuma ku bi Allah da taƙawa. Lalle, Allah, Mai tsananin uƙũba ne. [Surah Al-Ḥashr: 7]

لَّقَدۡ كَانَ لَكُمۡ فِي رَسُولِ ٱللَّهِ أُسۡوَةٌ حَسَنَةٌ لِّمَن كَانَ يَرۡجُواْ ٱللَّهَ وَٱلۡيَوۡمَ ٱلۡأٓخِرَ وَذَكَرَ ٱللَّهَ كَثِيرٗا

Lalle, abin kõyi mai kyau ya kasance gare ku daga Manzon Allah, ga wanda ya kasance yanã fãtan rahamar Allah da Rãnar Lãhira, kuma ya ambaci Allah da yawa. [Surah Al-Aḥzāb: 21]

Wannan aya raddi ce ga masu cewa a yi watsi da duk littattafan hadisai a kama irin koyarwarsu da Shaiɗanu suka ɗora su akai, irin su Mai Tatsine da yaransa.

Annabi shine wanda Allah Ya ce "ya ce":

قُلۡ أَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُواْ ٱلرَّسُولَۖ فَإِن تَوَلَّوۡاْ فَإِنَّمَا عَلَيۡهِ مَا حُمِّلَ وَعَلَيۡكُم مَّا حُمِّلۡتُمۡۖ وَإِن تُطِيعُوهُ تَهۡتَدُواْۚ وَمَا عَلَى ٱلرَّسُولِ إِلَّا ٱلۡبَلَٰغُ ٱلۡمُبِينُ

Ka ce: "Ku yi ɗã'ã ga Allah kuma ku yi ɗã'ã ga Manzo. To, idan kun jũya, to, a kansa akwai abin da aka aza masa kawai, kuma a kanku akwai abin da aka aza muku kawai, Kuma idan kun yi masa ɗã'ã za ku shiryu. Kuma bãbu abin da yake a kan Manzo fãce iyarwa (isarwa) bayyananna." [Surah An-Nūr: 54]

Lallai Annabi Muhammadu SAW Manzo ne, kuma ya isar da manzacinsa har lokacin da ya yiwa Sahabbansa khudubar ban kwana lokacin Hajjin ban kwana, a ƙarshe ya ke tambayar Sahabbai; "Shin a Ranar Tashin Ƙiyama idan an tambaye ku game da Ni me za ku faɗa?" Sahabbai suka amsa masa da cewa za su ce a Ranar "Lallai kai Manzon Allah ne kuma ka isar da Saƙon da aka baka don isarwa". (Da jin amsar Sahabbai), Sai Manzon Allah ya ɗaga ɗan yatsarsa manuniya zuwa sama sannan yayi nuni ga Sahabbai ya ce "Ya Allah Ka shaida, Ya Allah Ka shaida, Ya Allah Ka shaida" har sau uku, (watau ya isar da saƙo ga waɗannan bayi naSa Sahabbai). Duba cikakken Hadithin (Hijjatul Wada'i) cikin Sahihul Muslim, Sunan Abi Dawood, da Sunan Ibn Majah.

Sannan Manzon Allah SAW ya ce a isar daga gareshi watau a sanar da al'umma wannan Addini kamar yadda yake daga gurin shi SAW.

عن عبد الله بن عمرو قال :قال رسول الله صلّى الله عليه وسلم بلغوا عني و لو آية

An karƃo daga 'Abdullahi bin 'Amr ya ce: Manzon Allah SAW ya ce "Ku isar daga gareni koda aya ɗaya ce". Daga Littafin Musnad Ashshihaab Mujalladi na ɗaya shafi na 387 Hadithi na 662.

Bayan wannan, ya ja kunnen al'umma da ɗai kada wani ya kuskura ya jingina masa ƙarya:

An karƃo daga Rib'iyi bin Hisham cewa ya ji Sayyiduna Aliyu RA cikin wata khuɗuba da ya ke bayarwa yace: Manzon Allah SAW ya ce "Kada ku faɗi ƙarya game da Ni, domin duk wanda ya faɗi ƙarya game da Ni zai shiga Wuta. Muslim ne ya rubuto.

An karƃo daga Abu Huraira RA ya ce : Manzon Allah SAW ya ce"Duk wanda ya yi mini ƙarya da gangan, ya tanadi wajen zamansa a Wuta". Muslim ne ya rubuto.

Wajejen ƙarshen rayuwarsa a doron ƙasar nan Manzon Allah SAW ya yiwa Sahabbansa babbar Nasiha:

Hadith (Nasihar Bankwana)

Hadithi daga baban Najihin Irbaɗi dan Sa'ariyata Allah Ya ƙara yadda a gareshi ya ce: Manzon Allah (SAW) ya wa'azantar damu da wani wa'azi mai girgiza zukata, kuma idanuwa suka kwaranyar da hawaye. Sai muka ce Ya RasululLahi wannan kamar wa'azin mai ban kwana (da duniya), to i mana wasiyya. Yace ina yi muku wasiyya da kuji tsoron Allah Mabuwayi Maɗaukaki, sannan ku ji, ku yi biyayya ga koda bawa ne aka shugabantar a kanku. Saboda duk wanda yayi tsahon rayuwa a cikinku zai ga saɓani da yawa (cikin wannan Addini), to na horeku da bin Sunnata da Sunnar Shiryayyun Khalifofi masu shiryarwa (Abubakar, Umar, Uthman da Aliyu, Allah Ya ƙ ara yadda da su). Ku yi riƙo gam-gam da fiƙoƙinku (ga waɗannan Sunnoni), sannan na hane ku da bin ƙirƙirarrun abubuwa, domin Lallai dukkan wani ƙirƙirarren abu ɓata ne". Dawud da Timidhi suka rubuto.

Hadithi (Rasuwarsa, SAW)

3536. An karɓo daga Uwar Muminai A'ishatu RA, Matar Manzon Allah SAW ta ce: Manzon Allah SAW ya rasu yana da shekaru sittin da shida. Bukhari

6509. An karɓo daga Uwar Muminai A'ishatu RA, Matar Manzon Allah SAW ta ce: Lokacin da Manzon Allah SAW yake cikin ƙoshin lafiya yakan ce: " Babu wani rai na Annabi da za a karɓa (rasuwa) face an nuna masa gidansa a Aljannah sannan a bashi zaɓin mutuwa ko rayuwa". Saboda haka lokacin da ya zo rasuwa SAW, kansa yana kan cinyata sai hankalinsa ya gushe (ya suma) na ɗan wani lokaci, sai kuma ya farfaɗo tare da ƙura idanuwansa ga rufin ɗaki, ya ce: "Ya Allah (tare) da maɗaukakin aboki". Sai na ce, "Kenan bai zaɓi ya zauna da mu ba, (watau ya zaɓi ya rasu tun da an nuna masa gidansa na Aljanna)". Sai na fahimta cewar wannan shine tabbatuwar Hadisin da shi Annabin ya ringa faɗa mana. Kuma wannan

shine ƙarshen abinda Annabi yayi furuci da shi kafin rasuwarsa SAW " Allahumma Rafiƙal 'A'alaa". Duba Ƙur'an Sura ta 4 aya ta 69. Sahih Bukhari

وَمَن يُطِعِ ٱللَّهَ وَٱلرَّسُولَ فَأُوْلَٰٓئِكَ مَعَ ٱلَّذِينَ أَنۡعَمَ ٱللَّهُ عَلَيۡهِم مِّنَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ وَٱلصِّدِّيقِينَ وَٱلشُّهَدَآءِ وَٱلصَّٰلِحِينَۚ وَحَسُنَ أُوْلَٰٓئِكَ رَفِيقٗا

Kuma waɗannan da suka yi ɗã'a ga Allah da Mazonsa, to, waɗannan sunã tãre da waɗanda Allah Ya yi ni'ima a kansu, daga annabãwa da mãsu yawan gaskatãwa, da masu shahãda da sãlihai. kuma waɗannan sun kyautatu ga zama abõkan tafiya. [Surah An-Nisāʾ: 69]

Allahu Akbar, Allahu Akbar, Allahu Akbar. Innaa lilLahi wa innaa ilaiHi raajiuun. Ya Allah Ka ƙara daɗin Salati da Tsira da Aminci ga AnnabinKa kuma ManzonKa Annabin Rahma, Muhammad ɗan 'AbdulLahi da Sahabbansa da Iyalansa baki ɗaya da ma ragowar Musulman da ke kan Hanya irin tasu har ya zuwa Ranar Tashin Ƙiyama.

3.5 Sahabbansa da Matansa:

Sahabi (Aboki, da turanci Friend ko Companion) shine wanda ya rayu lokacin da Annabi yake da rai, amma da Sharaɗin:

1) Ya kusanci Annabi ko ya zauna dashi, tare da yin Imani da shi, da taimaka masa cikin Da'awah kuma ya rayu ya mutu akan haka. Waɗannan su ake kira makusantan Sahabbai. Suna daga cikin Muhajiruun da Ansaar. Allah Ya ƙara yadda da su.

2) Ya ganshi ko ya rubuto daga gareshi a zamaninsa, tare da Imani da shi, kuma ya rayu ya mutu akan haka.

3) Ya ji maganarsa amma bai ganshi ba saboda makanta kuma yayi Imani da shi, ya rayu kuma ya mutu akan haka.

4) Idan bai ganshi ba, bai ji maganarsa ba, amma ya rayu lokacin da Annabi ya ke da rai, kuma yayi Imani da shi, har ya mutu akan hakan, shima ana kiransa Sahabi amma na nesa kamar Najashi shugaban Habasha.

Saboda haka, duk wanda ya yi zamani da Annabi SAW, amma bai yi Imani da kiransa ba, ko ya zama munafuki, ko ya yaƙi Manzon Allah SAW da Sahabbansa, to ba za a kira shi da Sahabi ba komai dangartakarsa da Manzon Allah SAW.

Tun kafin zuwan Manzon Allah SAW, Allah AWJ Ya bayar da labarin zuwansa, haka Ya bayar da Labarin Sahabbansa da kuma Siffarsu cikin Linjila da Attaura.

مُّحَمَّدٌ رَّسُولُ ٱللَّهِۚ وَٱلَّذِينَ مَعَهُۥٓ أَشِدَّآءُ عَلَى ٱلْكُفَّارِ رُحَمَآءُ بَيْنَهُمْۖ تَرَىٰهُمْ رُكَّعًا سُجَّدًا يَبْتَغُونَ فَضْلًا مِّنَ ٱللَّهِ وَرِضْوَٰنًاۖ سِيمَاهُمْ فِى وُجُوهِهِم مِّنْ أَثَرِ ٱلسُّجُودِۚ ذَٰلِكَ مَثَلُهُمْ فِى ٱلتَّوْرَىٰةِۚ وَمَثَلُهُمْ فِى ٱلْإِنجِيلِ كَزَرْعٍ أَخْرَجَ شَطْـَٔهُۥ فَـَٔازَرَهُۥ فَٱسْتَغْلَظَ فَٱسْتَوَىٰ عَلَىٰ سُوقِهِۦ يُعْجِبُ ٱلزُّرَّاعَ لِيَغِيظَ بِهِمُ ٱلْكُفَّارَۗ وَعَدَ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ مِنْهُم مَّغْفِرَةً وَأَجْرًا عَظِيمًا

Muhammadu Manzon Allah ne. Kuma waɗannan (Sahabbansa) da ke tãre da shi mãsu tsanani ne a kan kãfirai, mãsu rahama ne a tsakãninsu, kanã ganin su sunã mãsu rukũ'i mãsu sujada, sunã nẽman falala daga Ubangijinsu, da yardarSa. Alãmarsu tanã a cikin fuskõkinsu, daga kufan sujuda. Wannan shĩ ne siffarsu a cikin Attaura. Kuma siffarsu, a cikin Injĩla ita ce kamar tsiron shũka wanda ya fitar da rẽshensa, sa'an nan ya ƙarfafa shi, ya yi kauri, sa'an nan ya daidaita a kan ƙafãfunsa, yanã bãyar da sha'awa ga mãsu shũkar' dõmin (Allah) Ya fusãtar da kãfirai game da su. Kuma Allah Ya yi wa'adi ga waɗanda suka yi ĩmãni, kuma suka aikata ayyukan ƙwarai, daga cikinsu, da gãfara da ijãra mai girma. [Surah Al-Fatḥ: 29]

Sahabbai, matan Manzon Allah SAW da yayansa, sune almajiran (ɗaliban) farko cikin wannan al'umma ga babbar makarantar Addini, wadda malaminta na farko shine Rasulullah, Fiyayyen halitta. Ya Allah Ka ƙara daɗin tsira da

aminci garesu baki ɗaya. Saboda haka dole muyi imani da cewar Sahabban Manzon Allah SAW mutane ne Adalai, na gari masu kyakkyawan hali, duk da cewar ba ma'asumai ba ne. Watau za su iya yin kuskure cikin ijtihadinsu.

Yadda Allah SWT Ya zaɓi Annabi cikin al'ummarsa da Manzanci da Annabci, haka kuma Ya zaɓa masa zaƙaƙuran abokanai masu adalci da amana da dattako da mutunci, haka Ya zaɓa masa Matan aure na gargari. Ba zai taɓa yiwuwa Annabi ya zama nagari, amma Sahabbansa da Matansa su zama gurɓatattu ba. Zargi ko zagin ɗaya daga cikinsu, to kana zargi ko zagin Allah ne da ManzonSa SAW. Kuma ka ƙaryata da yawa, daga cikin ayoyin Allah SWT da Hadisan Manzon Allah SAW. Domin Allah Ya ce Ya yarda da su, suma sun yarda da Allah. Haka Annabi SAW.

Sun taimakawa Annabi cikin rayuwarsa gaba ɗaya. Sun aura daga gidansa, shima ya aura daga gidajensu SAW. Annabi SAW yaga ƙarfin Imaninsu da gaskiyar aikinsu da jajircewarsu. Sun sadaukar da dukiyarsu da rayuwarsu domin ɗaukaka Addinin Allah SWT. Saboda haka Annabi ya yarda da su kuma ya yabesu, haka Allah SWT Ya yarda da su, suma sun yarda da Shi, Ya yabesu, Ya gafarta musu, kuma Ya yiwa da yawa busharar Aljanna tun anan Duniya ta bakin Fiyayyen halitta SAW. Alhamdu lilLah.

Koda yake an sami munafukai cikin wasunsu, da sukayi zamani da Manzo, to waɗannan dama ai Musulmai ne a baki amma Allah SWT Ya san kafirai ne a zuci. Kuma sun barranta da abokantakar Manzo. Watau ba za a kiraye su da Sahabbai ba, domin ba su yi imani matuƙar imani ba. Waɗannan wasu ƙidayayyun mutane ne cikin tawagar Manzo waɗanda Allah Ya tsinkayar da Manzo ga al'amarinsu, sannan Manzo ya faɗawa Sahibin Sirrinsa. Allah Ka kiyayemu da kasancewa munafukai.

Shaidar da Allah SWT Ya yiwa Sahabbai:

كُنتُمۡ خَيۡرَ أُمَّةٍ أُخۡرِجَتۡ لِلنَّاسِ تَأۡمُرُونَ بِٱلۡمَعۡرُوفِ وَتَنۡهَوۡنَ عَنِ ٱلۡمُنكَرِ وَتُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِۗ وَلَوۡ ءَامَنَ أَهۡلُ ٱلۡكِتَٰبِ لَكَانَ خَيۡرًا لَّهُمۚ مِّنۡهُمُ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ وَأَكۡثَرُهُمُ ٱلۡفَٰسِقُونَ

Kun kasance mafi alhẽrin al'umma wadda aka fitar ga mutãne kuna umurni da alhẽri kuma kunã hani daga abin da ake ƙi, kuma kunã ĩmãni da Allah. Kuma dã Mutãnen Littãfi (Yahudu da Kirista) sun yi ĩmãni, lalle ne, dã (haka) yã kasance mafi alhẽri a gare su. Daga cikinsu akwai mũminai (waɗanda suka karɓi Musulunci), kuma mafi yawan su fãsiƙai ne. [Surah Āli-ʿImrān: 110]

وَٱلسَّٰبِقُونَ ٱلۡأَوَّلُونَ مِنَ ٱلۡمُهَٰجِرِينَ وَٱلۡأَنصَارِ وَٱلَّذِينَ ٱتَّبَعُوهُم بِإِحۡسَٰنٖ رَّضِيَ ٱللَّهُ عَنۡهُمۡ وَرَضُواْ عَنۡهُ وَأَعَدَّ لَهُمۡ جَنَّٰتٖ تَجۡرِي تَحۡتَهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدٗاۚ ذَٰلِكَ ٱلۡفَوۡزُ ٱلۡعَظِيمُ

Kuma mãsu tsẽrẽwa na farko daga Muhãjirina da Ansar da waɗanda suka bi su da kyautatãwa, Allah Ya yarda daga gare su su kuma sun yarda daga gare Shi, kuma Ya yi mãsu tattalin gidãjen Aljanna; Kõramu sunã gudãna a ƙarƙashinsu, suna madawwamã a cikinsu har abada. Wancan ne babban rabo mai girma. [Surah At-Tawbah: 100]

Wannan babbar shaida ce daga Allah ga Sahabban Manzo. Lokacin da aka saukar da wannan aya, suwaye Annabi yake faɗawa da lamirin "kuntum"? Ko shakka babu Sahabbansa na kusa da na nesa da iyalan gidansa duk yake faɗawa. Saboda haka a sami wasu la'anannu su ringa aibatawa da zagin Sahabbai da matan Manzon Allah SAW, ba ƙaramin cin fuska bane ga Musulunci da Musulmai baki ɗaya. Allah Ya isa.

Idanma sunyi wani kuskure to Allah Ya ce musu;

لَّقَد تَّابَ ٱللَّهُ عَلَى ٱلنَّبِيِّ وَٱلۡمُهَٰجِرِينَ وَٱلۡأَنصَارِ ٱلَّذِينَ ٱتَّبَعُوهُ فِي سَاعَةِ ٱلۡعُسۡرَةِ مِنۢ بَعۡدِ مَا كَادَ يَزِيغُ قُلُوبُ فَرِيقٖ مِّنۡهُمۡ ثُمَّ تَابَ عَلَيۡهِمۡۚ إِنَّهُۥ بِهِمۡ رَءُوفٞ رَّحِيمٞ

وَعَلَى ٱلثَّلَٰثَةِ ٱلَّذِينَ خُلِّفُواْ حَتَّىٰٓ إِذَا ضَاقَتۡ عَلَيۡهِمُ ٱلۡأَرۡضُ بِمَا رَحُبَتۡ وَضَاقَتۡ عَلَيۡهِمۡ أَنفُسُهُمۡ وَظَنُّوٓاْ أَن لَّا مَلۡجَأَ مِنَ ٱللَّهِ إِلَّآ إِلَيۡهِ ثُمَّ تَابَ عَلَيۡهِمۡ لِيَتُوبُواْۚ إِنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلتَّوَّابُ ٱلرَّحِيمُ

Lalle ne, haƙĩƙa, Allah Ya karɓi tũbar Anbabi da Muhãjirĩna da Ansãr waɗanda suka bĩ shi, a cikin sã'ar tsanani, daga bãya zukãtan wani ɓangare daga gare su sun yi kusa su karkata, sa'an nan (Allah) Ya karɓi tũbarsu. Lalle, Shĩ ne Mai tausayi, Mai jin ƙai gare su.

Kuma (Allah) Yã karɓi tũba a kan ukun nan waɗanda aka jinkirtar har ƙasa da yalwarta ta yi ƙunci a kansu, kuma rãyukansu suka yi ƙunci a kansu, kuma suka yi zaton bãbu wata mafakã daga Allah fãce (kõmãwa) zuwa gare Shi. Sa'an nan Allah Ya karɓi tũbarsu, dõmin su tabbata a kan tũba. Lalle Allah ne Mai karɓar tũba, Mai jin ƙai. [Surah At-Tawbah: 117-118]

Ga matan Annabi kuwa Allah SWT cewa yayi;

Ummuhatul Muminina.

ٱلنَّبِىُّ أَوۡلَىٰ بِٱلۡمُؤۡمِنِينَ مِنۡ أَنفُسِهِمۡۖ وَأَزۡوَٰجُهُۥٓ أُمَّهَٰتُهُمۡۗ وَأُوْلُواْ ٱلۡأَرۡحَامِ بَعۡضُهُمۡ أَوۡلَىٰ بِبَعۡضٍ فِى كِتَٰبِ ٱللَّهِ مِنَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ وَٱلۡمُهَٰجِرِينَ إِلَّآ أَن تَفۡعَلُوٓاْ إِلَىٰٓ أَوۡلِيَآئِكُم مَّعۡرُوفٗاۚ كَانَ ذَٰلِكَ فِى ٱلۡكِتَٰبِ مَسۡطُورٗا

Annabi ne mafi cancanta ga mũminai bisa ga su kansu, kuma mãtansa uwãyensu ne. Kuma ma'abuta zumunta waɗansunsu sun fi waɗansu a cikin Littãfin Allah bisa ga mũminai da Muhãjirai, fãce fa idan kun aikata wani alhẽri zuwa ga majiɓintanku. Wancan yã kasance a cikin Littafi, rubũtacce. [Surah Al-Aḥzāb: 6]

يَٰنِسَآءَ ٱلنَّبِيِّ لَسۡتُنَّ كَأَحَدٖ مِّنَ ٱلنِّسَآءِۚ إِنِ ٱتَّقَيۡتُنَّۚ فَلَا تَخۡضَعۡنَ بِٱلۡقَوۡلِ فَيَطۡمَعَ ٱلَّذِى فِى قَلۡبِهِۦ مَرَضٞ وَقُلۡنَ قَوۡلٗا مَّعۡرُوفٗا

وَقَرْنَ فِي بُيُوتِكُنَّ وَلَا تَبَرَّجْنَ تَبَرُّجَ ٱلْجَـٰهِلِيَّةِ ٱلْأُولَىٰ ۖ وَأَقِمْنَ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتِينَ ٱلزَّكَوٰةَ وَأَطِعْنَ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥٓ ۚ إِنَّمَا يُرِيدُ ٱللَّهُ لِيُذْهِبَ عَنكُمُ ٱلرِّجْسَ أَهْلَ ٱلْبَيْتِ وَيُطَهِّرَكُمْ تَطْهِيرًا

وَٱذْكُرْنَ مَا يُتْلَىٰ فِي بُيُوتِكُنَّ مِنْ ءَايَـٰتِ ٱللَّهِ وَٱلْحِكْمَةِ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ لَطِيفًا خَبِيرًا

Yã mãtan Annabĩ! Ba ku zama kamar kõwa ba daga mãtã, idan kun yi taƙawa, sabõda haka, kada ku sassautar da magana, har wanda ke da cũta a cikin zuciyarsa ya yi ɗammani, kuma ku faɗi magana ta alheri.

Kuma ku tabbata a cikin gidãjenku, kuma kada ku yi fitar gãye-gãye irin fitar gãye-gãye ta jãhiliyyar farko. Kuma ku tsaĩ da salla, kuma ku bãyar da zakka, ku yi ɗã'ã ga Allah da ManzonSa. Allah na nufin Ya tafiyar da ƙazamta kawai daga gare ku, yã mutãnen Babban Gida! Kuma Ya tsarkake ku, tsarkakẽwa.

Kuma ku tuna abin da ake karantawa a cikin ɗãkunanku daga ãyõyin Allah da hukunci. Lalle Allah Yã kasance Mai tausasãwa Mai labartawa. [Surah Al-Aḥzāb: 32-34]

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ قُل لِّأَزْوَٰجِكَ وَبَنَاتِكَ وَنِسَآءِ ٱلْمُؤْمِنِينَ يُدْنِينَ عَلَيْهِنَّ مِن جَلَـٰبِيبِهِنَّ ۚ ذَٰلِكَ أَدْنَىٰٓ أَن يُعْرَفْنَ فَلَا يُؤْذَيْنَ ۗ وَكَانَ ٱللَّهُ غَفُورًا رَّحِيمًا

Yã kai Annabi! Ka ce wa mãtan aurenka da 'yã'yanka da mãtan mũminai su kusantar da ƙasã daga manyan tufãfin da ke a kansu. Wancan ya fi sauƙi ga a gane su dõmin kada a cũce su. Kuma Allah Yã kasance Mai gãfara, Mai Jin ƙai. [Surah Al-Aḥzāb: 59]

Ƙazafin da Munafukai suka yiwa Nana A'isha RA

Ƙazafin da aka yiwa Uwar Muminai kuwa, wadda duk Sahabbai da Annabi suka shiga cikin damuwa, damuwa mai tsanani amma banda munafukai,

domin sune suka kururuta wutar wannan ƙazafi. Wannan ya nuna Annabi bai san gaibu ba, har sai da aka jira bayan yan kwanaki, Allah SWT Ya saukar da ayoyi har guda goma cikin Alƙur'ani domin tsarkake ta daga abinda munafukai suka ƙala mata.

إِنَّ ٱلَّذِينَ جَآءُو بِٱلْإِفْكِ عُصْبَةٌ مِّنكُمْ ۚ لَا تَحْسَبُوهُ شَرًّا لَّكُم ۖ بَلْ هُوَ خَيْرٌ لَّكُمْ ۚ لِكُلِّ ٱمْرِئٍ مِّنْهُم مَّا ٱكْتَسَبَ مِنَ ٱلْإِثْمِ ۚ وَٱلَّذِى تَوَلَّىٰ كِبْرَهُۥ مِنْهُمْ لَهُۥ عَذَابٌ عَظِيمٌ

لَّوْلَآ إِذْ سَمِعْتُمُوهُ ظَنَّ ٱلْمُؤْمِنُونَ وَٱلْمُؤْمِنَٰتُ بِأَنفُسِهِمْ خَيْرًا وَقَالُوا۟ هَٰذَآ إِفْكٌ مُّبِينٌ

لَّوْلَا جَآءُو عَلَيْهِ بِأَرْبَعَةِ شُهَدَآءَ ۚ فَإِذْ لَمْ يَأْتُوا۟ بِٱلشُّهَدَآءِ فَأُو۟لَٰٓئِكَ عِندَ ٱللَّهِ هُمُ ٱلْكَٰذِبُونَ

وَلَوْلَا فَضْلُ ٱللَّهِ عَلَيْكُمْ وَرَحْمَتُهُۥ فِى ٱلدُّنْيَا وَٱلْـَٔاخِرَةِ لَمَسَّكُمْ فِى مَآ أَفَضْتُمْ فِيهِ عَذَابٌ عَظِيمٌ

إِذْ تَلَقَّوْنَهُۥ بِأَلْسِنَتِكُمْ وَتَقُولُونَ بِأَفْوَٰهِكُم مَّا لَيْسَ لَكُم بِهِۦ عِلْمٌ وَتَحْسَبُونَهُۥ هَيِّنًا وَهُوَ عِندَ ٱللَّهِ عَظِيمٌ

وَلَوْلَآ إِذْ سَمِعْتُمُوهُ قُلْتُم مَّا يَكُونُ لَنَآ أَن نَّتَكَلَّمَ بِهَٰذَا سُبْحَٰنَكَ هَٰذَا بُهْتَٰنٌ عَظِيمٌ

يَعِظُكُمُ ٱللَّهُ أَن تَعُودُوا۟ لِمِثْلِهِۦٓ أَبَدًا إِن كُنتُم مُّؤْمِنِينَ

وَيُبَيِّنُ ٱللَّهُ لَكُمُ ٱلْـَٔايَٰتِ ۚ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ

إِنَّ ٱلَّذِينَ يُحِبُّونَ أَن تَشِيعَ ٱلْفَٰحِشَةُ فِى ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ لَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ فِى ٱلدُّنْيَا وَٱلْـَٔاخِرَةِ ۚ وَٱللَّهُ يَعْلَمُ وَأَنتُمْ لَا تَعْلَمُونَ

وَلَوْلَا فَضْلُ ٱللَّهِ عَلَيْكُمْ وَرَحْمَتُهُۥ وَأَنَّ ٱللَّهَ رَءُوفٌ رَّحِيمٌ

FASSARA

Lalle ne waɗanda suka zo da ƙiren ƙarya waɗansu jama'a ne daga gare ku, kada ku yi zatonsa sharri ne a gare ku. Ã'a, alhẽri ne gare ku. Kõwane mutum daga gare su na da sakamakon abin da ya sanã'anta na zunubi, kuma wanda ya jiɓinci girmansa, daga gare su, yanã da azãba mai girma.

Don me a lõkacin da kuka ji shi mũminai maza da mũminai mãta ba su yi zaton alhẽri game da kansu ba kuma su ce: "Wannan ƙiren ƙarya ne bayyananne?"

Don me ba su zo da shaidu huɗu a kansa ba? To idan ba su kãwo shaidun nan ba to, waɗannan, a wurin Allah, sũ ne maƙaryata.

Kuma bã dõmin falalar Allah ba a kanku da rahamarSa a cikin dũniya da Lãhira. Lalle ne, dã azãba mai girma ta shãfe ku a cikin abin da kuka kũtsa da magana a cikinsa.

A lõkacin da kuke marãbarsa da harsunanku kuma kunã cẽwa da bakunanku abin da bã ku da wani ilmi game da shi, kuma kunã zaton sa mai sauƙi alhãli kuwa, shi a wurin Allah, babba ne.

Kuma don me a lõkacin da kuka ji shi, ba ku ce ba, "Bã ya yiwuwa a gare mu, mu yi magana a game da wannan. Tsarki ya tabbata a gare Ka, wannan ƙiren ƙarya ne mai girma"?

Allah Yanã yi muku wa'azi, kada ku kõma ga irinsa, har abada, idan kun kasance mũminai.

Kuma Allah Yanã bayyana muku ãyõyin Sa, kuma Allah Masani ne, Mai hikima.

Lalle ne waɗanda ke son alfãsha ta wãtsu ga waɗanda suka yi ĩmãni sunã da azãba mai raɗaɗĩ a cikin dũniya da Lãhira. KumaAllah, Shi ne Ya sani, alhãli kuwa, kũ ba ku sani ba.

Kuma bã dõmin falalar Allah ba a kanku da rahamar Sa. Kuma lalle ne Allah Mai tausayi ne, Mai jin ƙai! [Surah An-Nūr: 11-20]

A ƙarshe Allah SWT Ya yi narko na La'ana (Tsinuwa) kan duk wanda ya ci gaba da aibantata da duk wata baiwar Allah katangaggiya gafila har ya zuwa Ranar Tashin Ƙiyama.

إِنَّ ٱلَّذِينَ يَرۡمُونَ ٱلۡمُحۡصَنَٰتِ ٱلۡغَٰفِلَٰتِ ٱلۡمُؤۡمِنَٰتِ لُعِنُواْ فِي ٱلدُّنۡيَا وَٱلۡأٓخِرَةِ وَلَهُمۡ عَذَابٌ عَظِيمٞ

يَوۡمَ تَشۡهَدُ عَلَيۡهِمۡ أَلۡسِنَتُهُمۡ وَأَيۡدِيهِمۡ وَأَرۡجُلُهُم بِمَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ

يَوۡمَئِذٖ يُوَفِّيهِمُ ٱللَّهُ دِينَهُمُ ٱلۡحَقَّ وَيَعۡلَمُونَ أَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلۡحَقُّ ٱلۡمُبِينُ

FASSARA

Lalle ne waɗannan da suke jĩfar mãtã mãsu kãmun kai gãfilai mũminai, an la'ane su, a cikin dũniya da Lãhira, kuma sunãda azãba mai girma.

A rãnar da harsunansu da hannãyensu, da ƙafãfunsu suke bãyar da shaida a kansu, game da abin da suka kasance sunã aikatãwa.

A rãnar dai Allah Yake cika musu sakamakonsu tabbatacce kuma sunã sanin (cẽwa) lalle Allah, Shi ne Gaskiya bayyananna. [Surah An-Nūr: 23 - 25].

Da wannan za mu iya tambayar Yan Shi'a ina suka kwana?

Daga cikin Sahabbai da Matan Manzon Allah SAW, akwai da yawa waɗanda Allah SWT Ya faɗawa Manzo da ya yi musu bushara da Aljannah. Banda waɗanda suka halarci yaƙin Badar cewar yan Aljanna ne dukkansu. Haka waɗanda suka yiwa Manzo mubaya'a ƙarƙashin bishiya a Hudaibiya, watau Bai'atu Ridwan, (Mubaya'ar samun Yardar Allah). Manzo SAW ya keɓance wasu cikin Hadisansa da cewa suma yan Aljanna ne. Matan

Manzon Allah SAW duk yan Aljanna ne, haka yayansa. Duk wannan ya baiyana cikin Ayoyin Alƙur'ani mai Tsarki da Hadisai ingantattu.

Goman da akaiwa bushara da Aljannah cikin hadisi guda sune: Abubakar, Umar, Uthman, Ali, Ɗalha bin 'Ubaidullahi, Azzubair binil 'Auwam, Sa'ad bin Abi Waƙƙas, Abdurrahmam bin 'Auf, Sa'id bin Zaid da Abu 'Ubaidata 'Amir bin Jarrah. Hadisai da yawa sun zo akan falalar ɗaiɗaikunsu da kuma gabaɗayansu. Allah Ya ƙara yarda a garesu.

Daga cikin waɗanda aka yiwa bushara da Aljannah akwai ɗai-ɗaikun mutane da suka zo cikin Hadisai daban-daban kamar su; Khadijah bint Khuwailid, matar Manzo kuma mahaifiyar Faɗima, yarta Faɗima, 'Aisha bint Abu Bakr itama matar Manzon Allah, Baraka Umm Aiman (yantacciyar baiwar Manzon Allah SAW), Ammar ibn Yaasir, Hamza ibn AbdulMuɗɗalab, Zaid ibn 'Amr, Salman al-Farisi, Thabit ibn Qais Al-ansari, Bilal Ibn Rabi'a, ‘Abdullah ibn Salaam, Ja‘far ibn Abi Ɗaalib da matar nan mai farfaɗiya da sauransu.

Waraqatu Ibn Naufal (abokin wasan Nana Khadijah ne, watau ɗan wan mahaifinta ne) shima Annabi SAW ya ce ɗan Aljanna ne. Waraqah Balarabe ne amma ya bar bautar gumaka kuma ya shiga Kiristanci na asali wanda bai yadda da "Trinity" ba, wai Allah uku ne. Saninsa da Bible sosai yasa ya gano tarihin zuwan Annabi SAW a ciki. Waraqah shine wanda Nana Khadijah ta ɗauki Manzon Allah SAW ta kai shi gabansa domin neman fatawar menene yake faruwa da shi Annabi, lokacin da aka fara yi masa Wahayi a cikin kogon Hira, kuma ya dawo gida yana mai jin tsoro da fargaba. Duk da Nana Khadijah ta kwantar masa da hankali SAW, cikin faɗinta "kai mai gaskiya ne, mai haƙuri, mai tausayin talakawa, mai sada zumunci, saboda haka Allah ba zai bari cuta ta shafe ka ba". To amma tashi mu je gurin ɗan uwana Waraqatu domin yana da ilimin Addinin Sama (Kiristancin Allah ɗaya ne kawai ba na ukun uku ba watau Trinity)".

Ta cewa Waraqah ga ɗan ɗan uwanka nan ga abinda ya sameshi. Waraqah ya tambayi Manzon Allah SAW, cewar "me ka gani kuma me ka ji?" Bayan Manzon Allah SAW ya faɗa masa abinda ya gani, da farkon Suratul 'Alaƙ

zuwa ayoyi biyar da aka fara saukarwa, sai waraƙah ya ce wannan ne Mala'ikan da ke kawo Saƙo ga Annabawa. Saboda haka kai Annabi ne, inama lokacin da mutanenka za su fidda kai daka garin ka, ina da ragowar ƙarfi, na bada gaskiya da kai kuma na taimakeka. Sai Annabi ya ce "Au har fitar da Ni za a yi daga gari?" Waraqah yace, ai babu wanda ya zo da irin saƙon ka a baya, face sai da ya sami ƴan adawa da abokan gaba. Amma bayan kwana kaɗan da wannan farkon Wahayi ga Manzon Rahama, Waraqah ya ce ga garin kunan - ya rasu.

Mu sani cewar Waraqatu ba ɗan Duba ba ne, ba kuma Matsafi ko Sufiy ba ne. A'a, masanin Addinin Kiristanci ne na Haƙiƙa. Bai faɗi KALMA ƙarara ba (koda yake ya faɗeta a sakaye, sannan a daidai wannan lokacin, ba a umarci Annabi da ya tashi ya yi kira ga Addini ba), bai yi Sallah ko sau ɗaya irin ta Musulmai ba (saboda ba a farlanta Sallah a lokacin ba), amma saboda ya yi Imani da Manzon Allah SAW (kuma da ya rayu har zuwa lokacin, da ya yi). Manzo SAW ya ce "Na yi mafarki da Waraqatu sanye da fararen kaya fes, saboda haka ɗan Aljanna ne. Da ba ɗan Aljanna ne ba, to da wasu nau'in kayan zan ganshi da su". Sahih Bukhari. Mun san kuma mafarkin Annabawa Gaske ne, saɓanin mafarkina da naka da nasa da na Shehunnai da Sufaye.

Haka aka yiwa waɗansu tarurrukan jama'a daban-daban irin wannan Bushara daga bakin da ba ya ƙarya, bakin Fiyayyen Halitta Bawan Allah kuma Manzon Allah Muhammad SAW.

Mahaifan Manzon Allah SAW sun rayu sun koma ga Mahaliccinsu kafin baiyanar Musulunci. A lokacin da suke raye, Addinai biyun da Allah Ya saukar watau Yahudanci da Nasarananci duk sun gurɓace da yawan ɗariƙoƙin maguzanci irin na Turawa da Asiya, sai ɗan abinda ba a rasa ba. Saboda haka Mahaifan Manzon Allah SAW suna cikin Ahlul Fitrah waɗanda al'amarinsu na ga Allah SWT. Akwai Hadisai daga Manzon Allah SAW dake nuni ga yadda Allah zai jarabe Jama’ar Fitrah a ranar sakamako, sannan Ya saka musu da abinda yafi dacewa da kowannensu. Sannan akwai Hadisi ingantace cikin Sahihu Muslim da yayi magana kan Mahaifiyar Manzon Allah SAW.

Hadith:

Abu Huraira yace: "Manzon Allah SAW ya ziyarci ƙabarin mahaifiyarsa sai ya zubar da hawaye (yayi kuka), waɗanda suke tare da shi suka zubar da hawaye suma. Sai ya ce: "Na roƙi Ubangijina izinin roƙa mata gafararSa, amma bai bani ba, sai na nemi izinin ziyarar ƙabarinta sai Ya bani izinin yin hakan. Saboda haka ku ziyarci ƙaburbura wannan zai tunatar da ku mutuwa"". Sahih Muslim 976.

Wannan Hadisi na da ban mamaki.

Na farko, babu wata aya ƙarara cikin Alƙur'ani da aka saukar bayan samuwar wannan hadisi akan mahaifiyar Manzon Allah SAW ko mahaifinsa, saɓanin abinda ya faru kan sha'anin Abu Ɗaalib, baffan Manzon Allah SAW kuma mahaifin Aliyu ibn Abu Ɗalib.

Na biyu, wannan lailai ya nuna sha'anin ko alamarin waɗanda suka rasu dab da zuwan Manzon Allah SAW, yana ga Allah SWT, Shi kaɗai ya san abinda ya tanadar musu.

Na uku, su Waɗan nan da suka rasu dab da aiko Manzon Allah SAW, in ka yi zaton suna da laifi to wanne iri ne? Babu dai Addini ingantacce wadda za su dogara da shi su bi (Yahudu sunce 'Uzairu ɗan Allah ne, Nasara sunce 'Isa ɗan Allah ne), kuma babu wanda aka aiko ɗin. Dan haka, kayi zaton suna da zunubi ba daidai ba ne, duk da suna cikin ɓata. Ta yiwu shi yasa aka hana Annabi wancan izinin na farko, domin sai an tabbatar da laifi za a nemi gafara. Sai cikin Rahamar Allah da jin ƙanSa, Ya turo ManzonSa Annabin Rahama domin fitar da al'umma daga cikin ruɗanin Addinai da duhun jahilcin Mushrikai.

Abu na huɗu, babu ta yadda Allah zai haɗawa ManzonSa masoyinSa baƙin ciki biyu. Na rashin gani da cikakken zama da mahaifansa biyu a duniya, kuma hakan ta daɗa kasancewa a Gobe ƙiyama. Saboda haka muna da kyakkyawan zaton Mahaifan Manzon Allah SAW suma suna Aljanna tare da shi in Sha Allah.

Manzon Allah SAW ya tashi Maraya cikakke. Mahaifinsa Abdullahi ibn AbdulMuɗɗalab ya rasu tun shi SAW yana cikin Mahaifiyarsa Aminatu bint Wahb. Ita kuma ta rasu SAW yana ɗan shekara shida. Saboda haka ya tashi ƙarƙashin kulawar baiwar mahaifinsa mai suna Baraka (Umm Aiman) da kakansa AbdulMuɗɗalab (wanda ya rasu SAW yana ɗan shekara takwas) da baffansa Abu Ɗaalib. Duk da waɗannan bayin Allah sun kula da shi matuƙar kulawa, amma rashin mahaifa ya sanya shi cikakken mai dogaro da Allah cikin duk rayuwarsa SAW. Wannan tasa ake kiransa da Mutawakkil (mai yawan dogaro ga Allah) SAW.

Daga cikin waɗanda Nassi na Alƙur'ani ko Hadisi ya tabbatar ɣan Wuta ne kuwa, akwai Abu Lahabi (baffan Annabi ne, ya cutar da Annabi matuƙar cutarwa), da duk kafiran da aka kashe a yaƙin Badar da Uhud da sauran yaƙoƙin da Manzo yayi, da munafukan lokacin Manzon Allah SAW, da Mahaifin Sayyidina 'Aliyu bin Abu Ɗalib (watau Abu Ɗaalib shima baffan Annabi ne, amma cikakken mai ƙaunar Annabi). Abu Ɗalib ya mutu yana mai ƙaunar Manzo - ƙauna ta gaske, amma sai dai kash, bai yi Imani da saƙon da aka aiko Manzo da shi ba. Wannan ƙaunar tasa shine mafi samun sassaucin Azaba a cikin Wutar Jahannama. Wannan kuma bai ragewa Sayyidina 'Ali wata daraja ba ga Manzon Allah SAW ko ga Allah SWT. Mun karanta ƙissar Annabi Ibrahim AS da mahaifinsa cikin Alƙur'ani mai Tsarki. Kuma mun san cewa lallai Annabi Ibrahim AS yafi 'Aliyu bin Abu Ɗalib daraja nesa ba kusa ba. Allah Shine Mai yawan yin abinda Ya so.

.

Hadith (Rasuwar Abu Ɗalib)

1360. An karɓo daga Al-Musaiyab: Lokacin da mutuwa ta kusa zuwa ga Abu Talib, sai Manzo Allah SAW ya tafi gurinsu kuma ya tarar da Abu Jahal bin Hisham da Abdullahi bin Umayyah bin Mugirah a gefensa. Manzon Allah SAW ya ce masa " Ya baffa na, ce "La ilaha illalLah" Kalmar da zan yi maka shaida gaba ga Allah (cewa ka mutu Musulmi)"". Abu Jahl da 'Abdullah bin Umaiyya suka ce "Ya Abu Talib shin za ka guji addinin Abdul Muɗɗalib ne?" Manzon Allah SAW Shi kuma ya ci gaba da kwaɗaitar da Abu Ɗalib da ya

faɗi KALMA, su kuma suka ci gaba da maimaita zancen su (na hana shi faɗar Kalma) har a ƙarshen maganarsa, Abu Ɗalib ya ce "yana kan Addinin Abdul Muɗɗalib (na bautawa gumaka ɗari uku da sittin dake cikin Ka'aba a lokacin), kenan ya ƙi faɗar Kalma. Sai Manzon Allah SAW ya ce, zan ci gaba da roƙa masa gafarar Allah matuƙar ba Allah ne ya hana Ni ba. Sai Allah Ya saukar da aya game da shi:

مَا كَانَ لِلنَّبِيِّ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَن يَسْتَغْفِرُواْ لِلْمُشْرِكِينَ وَلَوْ كَانُوٓاْ أُوْلِى قُرْبَىٰ مِنۢ بَعْدِ مَا تَبَيَّنَ لَهُمْ أَنَّهُمْ أَصْحَٰبُ ٱلْجَحِيمِ

Bã ya kasancẽwa ga Annabi da waɗanda suka yi ĩmãni, su yi istigifãri ga mushirikai, kuma kõ dã sun kasance ma'abũta zumunta ne daga bãyan sun bayyana a gare su, cẽwa lalle ne, sũ, 'yan Jahĩm ne. [Surah At-Tawbah: 113]. Sahih Bukhari.

Saboda haka, Musulmi ya daina ruɗuwa da bin wani Shehi ko Wali ko wani Shugaban ɗariƙa wai zai bashi Aljanna ko Ranar Ƙiyama zai yi sumogal ɗinsa cikin Aljanna. Kuma duk son da kake yiwa Manzon Allah SAW, idan baka yi masa biyayya cikin duk abinda ya zo da shi ba, to ka taɓe Duniya da Lahira. Haka duk irin ambaton ka da KALMA, idan ka yi abinda ya rusa KALMAR, to ka taɓe Duniya da Lahira.

Manzon Allah SAW ya sake jan kunnen Sahabbai (da duk waɗanda za su zo bayansu):

Hadith (Jan kunne kan zagin Sahabbai)

Daga Abu Huraira RA yace, Manzon Allah SAW yace "Kada ku zagi Sahabbai na, Na rantse da Wanda raina yake HannunSa, da ɗaya daga cikinku zai ciyar da dukiya gwargwadon zinare girman dutsen Uhud, to ba zai yi daidai da ladan mudunnabi ɗaya kai ko rabin ɗaya da Sahabina ya ciyar ba (duk a tafarkin Allah). Sahih Bukhari da Sahih Muslim.

An karɓo daga Abdullahi ɗan Mas'ud yace, Manzon Allah SAW yace "Mutanen da suke cikin ƙarnina, su suka fi nagarta (alkhairi), sai ƙarni mai bi masa, sannan ƙarnin dake binsa". (Gwargwadon shekaru ɗari uku kenan) Sahih Bukhari da Sahih Muslim.

Saboda haka duk abinda bai zama Addina ba, cikin waɗacan ƙarnonin, to duk kyansa a yau, ba zai taɓa zama Addina ba.

Ina yan ƙala ƙato masu cewa ayi watsi da jawaban Sahabbai na dangane da bayanan Annabi SAW da yayi musu a cikin wannan Addini namu? Ina yan Shi'a masu la'antar Sahabbai da matan Manzo? Shin ba sa karanta irin waɗannan Hadisan ne ko kuwa Shaiɗan ne ya riga yayi musu fitsari a ƙa? Allah Ya sauwaƙe.

3.6 Musuluncin:

".....A yau Nã kammalã muku addininku, Kuma Nã cika ni'imaTa a kanku, Kuma Nã yarda da Musulunci ya zama addini a gare ku....." Ma'ida aya ta 3.

Wannan aya an saukar da ita ranar Arafat shekarar Hajin ban kwana.

Musulunci shine faɗin ka "La ilaha illalLah, Muhammadur RasululLah". Wannan ita ake cewa Kalmar Shahada. Da ita ake shiga Musulunci, kuma ta ƙunshi ɓangare biyu; na farko janibin Allah AWJ, na biyu janibin Manzon Allah SAW.
Ma'ana:

1) Babu wani abinda ya cancanci a bauta masa face Allah Shi kaɗai. Shi kaɗai zai Shar'anta a yi, a yi, a bari, a bari, tare da ƙauna girmamawa, tsarkakewa, fatan samun rahama da jin ƙai da tsoron fushinSa da azabarSa JJH. Duk wannan Shari'a tana ƙunshe cikin Alƙur'ani mai Tsarki.

2) Babu da ɗai wani da zai koyar da wannan Ibada ta bauta face wanda aka aiko shi da ita, watau Manzon Allah SAW. Duk bayanan da Manzon Allah SAW ya yi domin fassara ma'anonin Alƙur'ani da aiki da shi, suna ƙunshe cikin Sunnar sa wadda aka rubuce cikin littattafan Hadisai. Dole a san shi SAW, kuma a so shi, ayi masa biyayya cikin duk umarni ko hanin da ya yi, a gaskata shi cikin duk abinda ya bada labari na gaibu da zahiri. Wallahi duk wanda ka bi cikin sha'anin Addini a yau, ba Manzon Allah SAW ba, ka kama ƙafar wala. Ka mutu ka halaka duniya da lahira. Allah Ya sauwaƙe.

3) Faɗin wannan Kalma ya ƙunshi kuma yin aiki da ita. Aiyukan nan kuma sun kasu kashi biyu - Ayyukan zuci na ɓoye (Imani da: Allah, Mala'iku, Manzanni, Littattafai, Ranar Ƙarshe, Ƙaddara mai kyau da maras kyau), da Ayyukan gaɓɓai na fili (Furta Kalma, Salla, Azumi, Zakka, Hajji). Ayyuka na fili, su suke nuni ga gaskiyar gasgatawar zuciyar mutum ga Musulunci. Ɗoriya kan wannan kuma sai kyautatawa cikin ayyukan can, watau Ihsani (yi domin Allah kamar kana ganinSa ga Shi gaba gareka), kuma bisa koyarwar Manzo Allah SAW kawai.

Dalili kan wannan shine, faɗin Allah SWT;

فَٱعۡلَمۡ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا ٱللَّهُ

Ka sani cewar babu abin bautawa da cancanta sai Allah..... Suratu Muhammad aya ta 19.

مُّحَمَّدٞ رَّسُولُ ٱللَّهِ

Muhammadu Manzon Allah ne. Fathi aya ta 29.

وَمَآ أُمِرُوٓاْ إِلَّا لِيَعۡبُدُواْ ٱللَّهَ مُخۡلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ حُنَفَآءَ وَيُقِيمُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَيُؤۡتُواْ ٱلزَّكَوٰةَۚ وَذَٰلِكَ دِينُ ٱلۡقَيِّمَةِ

Kuma ba a umarce su da kome ba fãce bauta wa Allah suna mãsu tsarkake addinin gare Shi, mãsu karkata zuwa ga addinin gaskiya, kuma su tsai da

salla kuma su bãyar da zakka, kuma wannan shi ne addinin waɗanda suke a kan hanyar ƙwarai. [Surah Al-Bayyinah: 5]

هُوَ ٱلۡحَيُّ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ فَٱدۡعُوهُ مُخۡلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَۗ ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ

Shĩ ne Mai rai (Wadda ba Ya mutuwa), bãbu abin bautãwa fãce Shi. Sabõda haka ku kira Shi, kunã mãsu tsarkake addini a gare Shi. Gõdiya ta tabbata ga Allah Ubangijin halittu. [Surah Ghāfir: 65]

Jan kunne kada a rarraba a zama ƙungiya ƙungiya.

Allah SWT cikin IliminSa Ya san za a rarrabu cikin Addini, a zama ƙungiya-ƙungiya shi yasa Ya ke ja mana kunne cikin littafinSa mai Tsarki.

وَأَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَلَا تَنَٰزَعُواْ فَتَفۡشَلُواْ وَتَذۡهَبَ رِيحُكُمۡۖ وَٱصۡبِرُوٓاْۚ إِنَّ ٱللَّهَ مَعَ ٱلصَّٰبِرِينَ

Kuma ku yi ɗã'a ga Allah da ManzonSa, kuma kada ku yi jãyayya har ku raunana kuma iskarku ta tafi, kuma ku yi haƙuri. Lalle ne Allah Yanã tãre da mãsu haƙuri. [Surah Al-Anfāl: 46]

وَلَا تَكُونُواْ كَٱلَّذِينَ تَفَرَّقُواْ وَٱخۡتَلَفُواْ مِنۢ بَعۡدِ مَا جَآءَهُمُ ٱلۡبَيِّنَٰتُۚ وَأُوْلَٰٓئِكَ لَهُمۡ عَذَابٌ عَظِيمٞ

Kuma kada ku kasance kamar waɗanda suka rarrabu kuma suka sãɓã wa jũna, bãyan hujjõji bayyanannu sun je musu kuma waɗannan sunã da azãba mai girma. [Surah Āli-ʿImrān: 105].

وَأَنَّ هَٰذَا صِرَٰطِي مُسۡتَقِيمٗا فَٱتَّبِعُوهُۖ وَلَا تَتَّبِعُواْ ٱلسُّبُلَ فَتَفَرَّقَ بِكُمۡ عَن سَبِيلِهِۦۚ ذَٰلِكُمۡ وَصَّىٰكُم بِهِۦ لَعَلَّكُمۡ تَتَّقُونَ

Kuma lalle wannan ne tafarkĩNa, yana madaidaici: Sai ku bĩ shi, kuma kada ku bi wasu hanyõyi, su rarrabu ku daga hanyãTa. Wannan ne Allah Ya yi muku wasiyya da shi tsammãninku, kunã yin taƙawa. [Surah Al-Anʿām: 153]

Sannan da faɗinsa Manzon Allah SAW (domin Allah Ya bashi "Jawami'ul kalimi" kalmomi taƙaitattu masu ɗauke da ɗunbun ma'ana), cikin Hadisansa:

Hadith. (Innamal a'amaalu binniyyaat.....)

An karɓo daga Abu Hafsin (Laƙabin Umar bin Khaɗɗaab, ana nufin baban Zaki saboda jaruntarsa), Umar ɗan Khaɗɗaab Allah Ya ƙara yadda a gareshi (RA) ya ce, ya ji Manzon Allah SAW ya ce "Da ɗai, ayyuka suna ɗamfare da niyyoyinsu ne, kuma lallai kowanne mutum akwai abinda yake fuskanta da niyyarsa, wanda hijirarsa ta kasance saboda Allah da ManzonSa ne (saboda Allah yayi kuma bisa koyi da koyarwar Manzon Allah SAW), to hijirarsa (ladan hijirarsa) tana ga Allah da ManzonSa (Allah ne Zai bashi lada saboda bin koyarwar Manzon Allah SAW), idan kuwa hijirarsa ta kasance ne domin wani abin duniya ko saboda mace da yake so ya aura, to hijirarsa tana ga wannan abinda ya niyyata (ba shi da lada gurin Allah AWJ)". Bukhari da Muslim suka rubuto. Wannan lafazin na Muslim ne tare da ƙarin bayanai na malamai cikin baka.

Ƙarin bayani ga wannan Hadisi

Wannan yana nuni da cewar kafin kowanne aiki na Ibada ya zama na gari kuma karɓaɓɓe gurin Allah SWT, sai an Niyyace shi da hakan, kuma Niyyar ta kasance ta cika SHARUƊA UKU -
(1) (Niyyar) Bin Umarnin Allah na ka yi, ko ka bari.

(2) (Niyyar) Yi ko barin domin Allah Shi kaɗai ba tare da riya ba.

(3) (Niyyar) Koyi da Manzon Allah SAW cikin yin aikin.

Mu sani cewar Niyya a zuci take, kuma ba a furuci da ita a cikin dukkan aikin Ibada, sai cikin wasu aiyuka ƙidayayyu kamar lokacin aikin Hajji. Wannan haka a ka samu a Sunnar Fiyayyen Halitta SAW.

Watau duk wata Ibada sai ta sami Umarnin Allah na a yi ta, kuma sai an nufi Allah da ita Shi kaɗai, sannan anyi koyi da Manzon Allah SAW shi kaɗai cikin yin ta, take karɓaɓɓiya a gurin Allah, wadda Allah zai bayar da lada domin ta Duniya da Lahira. Duk wanda yayi aiki guda ɗaya mai kyau, yana da lada goma, daga bakin da baya ƙarya, watau bakin Manzon Allah SAW.

Amma kaga Ibadar da bata cika waɗannan Sharuɗa uku ba, to komai kyanta in har tana da shi, watsatstsiya ce gurin Allah AWJ. Ka yarda ko kar ka yarda wannan kai ta shafa. Misali karanta salatul fatih, karanta salatut Tananjina, Hizb Bahr, maulidin Annabi SAW, maulidin Tijjani da na Inyasi, ziyara ta ƙabarburan Waliyai da Shehunnai a Kano, Bauchi, Sakkwato da Kaulaha da sauransu. Duk waɗannan babu inda Allah ko ManzonSa suka yi umarni da yi, ko suka sami koyarwar Manzon Allah SAW.

Hadith. (Iz ɗala'a 'Alaina Rajulun.....)

An dai karbo daga Amirul Mu'uminin Umar dan Khaddab RA yace:
Wata rana muna zaune da Manzon Allah SAW, sai ga wani mutum ya zo mana, tufafinsa fari kal, gashin kansa baki wuluk, babu wata alamar tafiya tattare da shi (kai ka ce mazaunin gari ne wadda bai yi wata tafiya ba), kuma babu daya daga cikinmu da ya sanshi. Sai ya tafi ya zauna gaban Manzon Allah SAW gwiwar sa na dungure da gwiwar Annabi, kuma ya dora tafukam hannayensa kan cinyoyinsa. Sai yace: Ya Muhammad fada mini menene Musulunci?

Manzon Allah SAW yace: "Musulunci shine shaidawa babu abin bautawa da cancanta sai Allah Shi kadai kuma Muhammad Manzon Allah ne, da tsayar da sallah, da bayar da zakka, da azumtar watan Ramadan, da hajjin dakin Allah ga wanda ya sami iko". Bakon yace ka fadi gaskiya. Sai muka yi mamakinsa domin yana tambayarsa kuma yana gasgata shi (watau dama

ya san amsar tambayar kenen). Bakon ya ci gaba da tamabaya ya ce: Bani bayanin menene Imani?

Manzon Allah SAW ya ce: “Imani shine yin Imani da Allah da Mala’ikunSa da LittattafanSa da ManzanninSa da Ranar Lahida da kuma yin Imani da Kaddara mai kyau da marar kyau”. Sai bakon ya ce ka yi gaskiya. Ya sake tambayarsa: Bani labarin menene Ihsani (kyautata aiki)? Annabi ya ce: “Ka bautawa Allah tamkar kana ganin Shi, domin in kai baka ganinShi to Shi Yana ganinka”. Yace bani labarin lokacin Tashin Kiyama. Annabi yace ai mai tambaya bai fi wanda ake tambaya sani ba, (watau dukkansu basu san ranar ba. Sai ya ce to fada mini alamominta. Annabi ya ce baiwa ta haifi uwargijiyarta, sannan za ka ga marasa takalma, talakawa marasa isashen tufafi makiyaya suna tsere wajen gina dogwayen gidaje. Sai mutumin ya tashi ya juya ya tafi. Ni (Umar) kuma sai na dan saurara tare da Manzon Allah SAW. Sai Manzon Allah SAW y ace: “Ya kai Umar, shin ka san mai tambayar can?” Sai nace: “Allah da ManzonSa ne suka fi sani”. Sai yace Jibrilu ne ya zo domin koya muku Addininku”. Muslim ne ya rubuto.

Ƙarin bayani ga wannan Hadisi:

Wannan Hadisi ya tattara dukkan bayanai kan Addinin Musuluncin. Idan ka koma cikin Alƙur'ani za ka ga duk dalilai ga waɗannan bayanan. Idan ka bada gaskiya ka furta KALMA, sai yin IMANI, sai ayyuka na gaɓɓai, - SALLAH, AZUMI, ZAKKAH, HAJJI, sai kuma Kyautatawa cikin duk waɗannan ayyuka watau IHSAN.

Duka waɗannan ayyuka da Allah Ya yi Umarnin a aikata su, dole abi koyarwar Manzon Allah SAW cikin aikata su. Idan ka bi wani cikin aikata su ba Manzon Allah SAW ba, kayi aikin banza kuma kana da zunubi. Shi ya sa nake ganin wauta da rashin kan ɣan ƙur'aniyyun da Ɣan Tatsine, da suke rajin sai a daina aiki da Hadisan (SUNNAR) Manzon Allah SAW (Koyarwarsa ga wannan Addini) da ta zo cikin Littattafan Hadisi irin su Sahihul Bukhari, Sahihu Muslim da sauransu. Wannan ba ƙaramar damƙewar basira ce ba. Waɗancan mutane sun yi watsi da karantarwar

Malam mai ahallari. Inda yace "ka yi koyi da malamai masu riƙo da SUNNAR Manzon Allah SAW). Idan baka karanta hadisi ba ta yaya zaka san SUNNAR Manzo? Allah Ya sauwaƙe Ya raba mu da ƙaramin sani wanda masu magana suka ce ƙuƙumi ne.

Hadith. (Man hadatha fi amrina.....)

Hadithi daga Uwar Muminai babar Abdullahi A'ishatu (matar Manzon Allah (SAW)) tace, Manzon Allah (SAW) ya ce "Duk wanda ya ƙirƙiri wani sabon abu a cikin wannan al'amarin namu (na Addini), wanda tun asali babu shi ciki to maidajje ne zuwa gareshi (baza a karɓa ba a matsayin Addini)". Bukhari da Muslim kuma hadithi na 5 cikin Arba'una Ahadith.

Ƙarin bayani ga wannan Hadisi:

Wannan kuwa ƙarara yake domin ya saɓawa ƙa'idojin aiki mai sunan "Aiki na gari karɓaɓɓe gurin Allah SWT", kamar yadda aka yi bayani nan sama kaɗan. Saboda kuma an riga an KAMMALA MANA WANNAN ADDINI tun Hajjin ban kwana, ranar Tsayuwar Arafah shekara ta goma da Hijrar Manzon Allah SAW daga Makka zuwa Madina. Yan bidi'a kun shiga uku, ku tuba ku dawo ga Addinin Musulunci, Sunnah Sak - Bidi'a Sam.

Hadith. (Innal halala baiyinun.....)

An karbo daga Abu Abdullahi An-Nu’man dan Bashir RA yace ya ji Manzon Allah SAW yace: “Lallai Halal a baiyane ta ke kuma Haramun ma a baiyane ta ke, kuma tsakaninsu akwai al’amura masu rikitarwa waɗanda da yawa daga cikin mutane basu sansu ba. Duk wanda ya kaucewa rikirkitattun abubuwa, ya tserar da Addininsa da kuma mutuncinsa. Wanda ya abka cikinsu kuwa to ya abka cikin Haram. Kamar mai kiyon dabbobi gefen shinge, bai aune ba sai dabbobinsa su abka cikin shingen. Ku saurara, lallai ga kowanne sarki akwai iyaka (ta mulkinsa), ku saurara, lallai iyakar Allah ita ce duk abinda Ya haramta. Ku saurara, tabbas a cikin jiki akwai wata tsoka,

idan ta gyaru dukkan jiki ya gyaru, idan ta ɓaci dukkan jiki ya ɓaci, ku saurara, ita ce ZUCIYA. Bukhari da Muslim.

Ƙarin bayani ga wannan Hadisi:

Bayan Umarni da Allah Ya yi domin yin aiki ga bauta maSa, sai kuma Hani da cewa kada a aikata wasu abubuwa masu cutarwa ga ɗan Adam, domin Allah babu wanda ya isa ya cutar da Shi da komai.

Waɗannan Halal da Haram duk Allah Ya baiyana su cikin Alƙur'ani mai Tsarki, sannan Sunnar Fiyayyen Halitta SAW ta ƙara haske a kai.

Tun wancan lokacin Manzon Allah SAW ya ce akwai rikirkitattun abubuwa ballantana yanzu da shaiɗanci ya ƙaru saboda tafiyar zamani, Allah Shine mai zamani. Jan kunnen shine ka gujewa duk wani rikirkitaccen al'amari domin ka zauna lafiya.

Misalin rikirkitattun abubuwa a wannan zamani sune kamar "Forex Trading" duba Littafi na mai suna "Daidai da Rashin Daidai kan Hadadar Kuɗaɗen Waje", da wani nau'i na mu'amalar ma'aurata na 69.

Wani sashi na Forex trading caca ce a ƙudundune. Shi kuwa mu'amalar ma'aurata ta 69 (kai da ƙafa), ta yadda shi zai ringa tanɗa da tsotson kan hancin butar ta (tsududu butar Allah, kanki na ƙasa ba kya zubda ruwa, cikinki damuna bayanki yabanya), ita kuma tana tanɗa da tsotson ɗan yatsarsa na wajen aljihun wando, ba ya cikin ɗabi'ar da Allah ya halicci mutum a kai. Sannan kalle-kallen fina-finai na fasiƙanci (blue Film) daga waɗanda ba Musulmai ba, shi ya haifar da duk irin wannan halaiyar cikin Musulmai.

Mahaɗin turmi sai taɓarya. Ko ɗan akuya sunsunawa kawai yake yi, sannan ya ci gaba da aiki. Duk da cewa ba inda aka ce halal ne ko haram ne, to gujewa wannan halaiyar shi ya fi kyau. Sannan wata matar, tana buɗe cinyoyinta, ɗoyin ruɓaɓben kifi ne kawai zai bugi hanci ka. Saboda haka, ko

kafi ɗan akuya da kare da zomo jaraba, ka haƙura da kai hacinka wajen. Allah Ya sauwaƙe.

Sannan mu sani cewar Manzon Allah SAW ya ce "Allah Ya la'anci duk mai kallon tsiraicin wani, sannan Allah Ya la'anci wanda ya bari ake ganin tsiraicinsa". Wannan kuwa ko a hoto ne marar motsi ballanta mai motsi da za a bijiro maka da komai tawai, ta yadda baka tsammani. Allah Ya gafarta mana.

Amma wannan haramci na ganin tsiraicin wani, bai shafi ma'aurata biyu a junansu ba, ko abinda mutum ya mallaka na bayi mata, waɗanda bai aurar da su ga wani ba (idan har yanzu da akwai).

Hadith (Ya gulaam inni u'allimuka kalimaat…….)

An karɓo daga Baban Abbas, Abdullahi ɗan Abbas RAm ya ce: Wata rana ina bayan Manzon Allah SAW akan abar hawarsa sai ya ce mini: "Ya kai wannan yaro, lallai zan sanar da kai wasu kalmomi; ka kiyaye Allah sai Ya baka kariya, ka kiyaye Allah sai ka same Shi gaba gareka, idan za ka yi roƙo, to roƙi Allah (Shi kaɗai), idan za ka nemi taimako, to nemi taimakon Allah Shi kaɗai, ka sani cewar, da duk al'umma za su taru domin su amfaneka da wani abu, to ba za su amfana maka da komai ba, face abinda Allah SWT Ya riga Ya ƙaddara maka. Da kuma za su taru domin su cutar da kai da wani abu, to ba za su iya ba, face da abinda Allah Ya ƙaddara maka tun farko. An ɗage alƙalami, takardu sun bushe. Tirmidhi ya rubuto.

Ƙarin bayani:

Wannan Hadithi yana nuni kan cewa lallai in ka kiyaye Allah cikin mu'amalarka da Shi da kuma ragowar bayinSa to lallai zai baka kariya ta ko'ina. Kiyaye Allah shine kiyaye dokokinSa na Umarni da Hani, a ɓoye da sarari. Wannan shi zai ƙara maka TAƘWA.

Abu na biyu shine, ba a roƙon kowa (cikin abinda Allah ne kawai zai iya yi, kamar samun haihuwa, lafiya, arziki da sauransu), ko Neman taimakon agajin gaggawa (kamar neman kariya daga faruwar wani mummunan abu da ake ganin gashinan gadan-gadan zai auku) ga kowa , sai Allah Shi kaɗai. Da wannan ne TAUHIDIN mutum yake daɗa ƙarfafuwa a cikin zuiyarsa. Yin wannan ga wanin Allah shi ake cewa SHIRKA. Ka yarda ko kar ka yarda wannan kai ta shafa.

Abu na uku shine, koya maka yin imani da ƘADDARA mai kyau da maras kyau. Tun ran gini ran zane in ji Bahaushe. Allahu Akbar kaji makarantar Manzon Allah SAW wadda waɗansu zindiƙai suke inkari.

Hadith. (Man kaz̲aba 'alaiya.....)

An karƀo daga Rib'iyi bin Hisham cewa ya ji Sayyiduna Aliyu RA cikin wata khuɗuba da ya ke bayarwa yace: Manzon Allah SAW ya ce "Kada ku faɗi ƙarya game da Ni, domin duk wanda ya faɗi ƙarya game da Ni zai shiga Wuta. Muslim ne ya rubuto.

Ƙarin bayani.

Allahu Akbar malam kaji koyarwar Fiyayyen Halitta. Ta yadda ya ɗaure kuma ya tsare Addinin Musulunci. Wannan shi ake kira da AMANAR ILIMI, ka bayar da shi yadda yake, babu ragi, babu ƙari. SAW.

Duk wanda ya ce Annabi ya ce kaza-da-kaza, alhali Annabin bai faɗa ba, to ya shiga uku, Wutar Jahannama ɗoɗar babu kwana babu taka burki.

Haka kuma, duk wanda Annabi ya riga ya faɗi kaza-da-kaza, amma ya ƙaryata, yace a'a Annabin bai ce kaza-da-kaza ɗin ba, To shima ya yiwa Annabin Rahma ƙarya, kuma Wutar Jahannama ita ce makomarsa ɗoɗar babu kwana babu jan burki.

Musussuka da ragowar yan ƙala ƙato masu ƙaramin sani ƙuƙumi ne da Sufaye (masu cewa Annabi ya basu wata Ibada a mafarki ko a baiyane ƙarara ko Masu da'awar wani Fathi (Ilhama ko Wahayi)) ina aka kwana? Allah Ya sauwaƙe.

Saboda haka Addinin Musulunci tuni yake a ƙaiyade. Babu ragi babu daɗi. Duk wanda zai yi magana kan Addinin Musulunci ya ji tsoron Allah, hujjarsa ta zama daga cikin Alƙur'ani da Sunnar Manzon Allah SAW. Idan babu stampi da goyon bayan Alƙur'ani ko Sunnar Fiyayyen Halitta, to Kasan cewar wannan abin "kitabur Ra'asi" ne watau molon ka ne kawai. Ya Allah! muna neman shiriya daga gareKa zuwa ga Hanya Madaidaiciya, da kariya daga faɗawa cikin hanyar da wasu mutane ke bi ta molon ka, babu Ayar Alƙur'ani babu Hadisin Manzon Allah SAW.

Hadith (Daga cikin khuɗubatul wada'i, khuɗubar ban kwana, lokacin Hajjin bankwana na Manzon Allah SAW cikin shekara to 10 da hijrah)..

Game da haramta jinnin fansa na lokacin faɗace-faɗacen Jahiliyya, cin riba, da umarni da kulawa da mata da umarni da riko da Kitab (Alƙur'ani).

An karbo daga Ja'far bin Muhammad wanda yace: Babanshi yace: Mun je wajen Ja’afar bin Abdullahi sai yake tambayar wadanda suka je domin ganin shi, har sai da zagaye ya zo kai na. Na ce nine Muhammad bin Ali bin Husain RA. Na ce masa fada mini game da Hajjin Manzon Allah SAW. Sai ya yi alama ga tara da hannunsa (watau ranar tsayuwar Arafah) sannan yace: Manzon Allah SAW ya zo kasan dutsen ya yiwa mutane khuduba da cewar:

“Hakika jininku, dukiyarku sun haramta kamar yadda wannan ranar taku take haramun, cikin wannan wata naku, a cikin wannan gari naku. Ku sani, duk wani abu na Jahiliyya na take shi ƙarƙashin ƙafata, ya zama Haramun (daga yau ɗin nan kuma a yanzu nan). Haramun shine ɗaukar jinin fansa na

lokacin Jahiliyya. Jini na fansa da muke bi wanda shine farkon wanda aka Haramta shine na ɗan Rabi'a bin Harith, wanda aka raine shi a cikin kabilar Sa'ad kuma Hudhail suka kashe shi. Haka Ribar Jahiliyya an sauke ta, kuma farkon ribarmu dana sauke ita ce ta 'Abbas bin 'Abdulmuɗɗallib. Ku ji tsoron Allah game da matanku. Hakika kun ɗauke su ne cikin kariyar Allah SWT, kuma jima'i (tarawa) da su halas ne da kalmomin Allah (Halaccin a cikin Alƙur'ani yake). Kuna da hakki a kansu na cewar kada su bar wani ya shiga gidajenku matuƙar baku aminta ba. Idan sun yi haka to ku tsawatar (doke su) musu amma tsawatarwa maras cutarwa. Su kuma hakkin su a kanku shine na ku basu abinci ku tufatar da su gwagwadon hali. Zan tafi (ma'ana zan rasu) in bari a tsakinku Littafin Allah, kuma idan kuka yi riko da shi, ba za ku taɓa ɓata ba. Kuma za a tambayeku game da ni (a Ranar Lahira), (ku faɗa mini) me za ku ce game da Ni? Duk jama'ar gurin suka ce: za mu bayar da shaidar cewa ka isar da sako ka aiwatar da Annabcinka kuma ka bayar da nasiha da jagoranci na gari. Mai bayar da labarin ya ce: sai Manzon Allah SAW ya ɗaga ɗan yatsarsa manuniya sama, sannan ya yi nuni ta ita (ɗan yatsar) ga jama'a yace musu: "Ya Allah ka shaida", "Ya Allah Ka shaida", har sau uku. Sahih Bukhari.

Game da haramta riba.

3334. An karɓo daga Sulaiman bin 'Amr, cewar babansa ya ce: "Na ji Manzon Allah SAW, lokacin Hajjin bankwana, ya ce: 'Duk Riba da ta samo asali daga jahiliyya an soke ta; kuna da uwar dukiyarku. Kada kuyi mu'amala ta rashin adalci, haka kada a yi muku mu'amala ta rashin adalci. Duk wani jini da ake bi na bashin faɗan ƙabilanci tun lokacin jahiliyya an soke shi, kuma jinin farko da na soke shine na Al-Harith bin 'Abdul-Muttalib wanda Banu Laith suka raine shi kuma Hudhail suka kashe shi.' Manzon Allah ya ce: 'Ya Allah, na isar (da saƙon)?' kuma suka ce (Sahabbai): 'Na'am' - sau uku. Ya ce SAW: "Ya Allah, Ka shaida!' har sau uku." (Hasan). Bukhari..

Game da biyan bashi

1265. Abu Umamah ya ce: "Lokacin Hajjin bankwana, Na ji Manzon Allah SAW yana cewa lokacin khuɗuba: 'Abinda aka ranta (ko aka ara) lallai a biya (ko mayar da shi), kuma mai lamuni shine da ɗaukar nauyi, kuma dai bashi dole a biya." (Hasan) At-Tirmidhi

Game da haramcin Jini, Dukiya, Mutunci da daukar laifi.

2159. Sulaimãn bin 'Amr bin Al-Ahwas ya hakaito daga babansa wanda ya ce: "Lokacin Hajjin bankwana, Na ji Manzon Allah SAW yana cewa: 'Wacce rana ce wannan?' Suka ce: 'Ranar Hajjin Babbar Sallah ce. Ya ce: 'Lallai Jininku da dukiyarku da mutuncinsu Haramcin ne ga kowannen ku, kamar yadda wannan Rana taku take Haramun a cikin wannan gari naku. Lallai, babu wani da zai ta'adda ci (ko zalunci) face alhakin abin yana kan shi. Lallai babu wani (uba) da zai yi ta'addanci kuma a riƙi ɗan sa da laifin. Haka da ba zai laifi ba a kama ubansa da laifin. Tabbas Ash-Shaiɗan ya fidda tsammanin za a bauta masa har abada a cikin wannan gari naku. AtTirmidhi.

3055. An karɓo daga Sulaiman bin 'Amr bin Ahwas cewa babansa ya ce " Na ji Manzon Allah SAW lokacin Hajjinsa na bankwana, ya ce: "Ya mutane na, wacce rana ce mafi Haramtuwa sau uku? Su ka ce, Ranar Babbar Hajji. Ya ce, Jininku da dukiyarku da mutuncinku Haramun ne kan kowannen ku kamar yadda wannan ranar taku take Haramun, a cikin wannan wata naku a cikin wannan ƙasa taku. Babu wani mai yin zunubi da zai aikata wani zunubi face alhakin zunubin yana kansa. Babu wani mutum da za a hora saboda zunubin mahaifinsa. Shaiɗan ya fidda tsammanin za a bauta masa har abada a wannan ƙasa taku. Amma za a yi masa biyayya kan ƙananan abubuwa marassa muhimmanci kuma zai wadatu da wannan kawai. Duk wani bashin Jini na faɗan ƙabilanci an soke shi (daga yau), kuma jinin farko da na soke shine na Harith bin Abdulmuɗallib, wanda aka raine shi cikin ƙabilar Laith kuma Hudhail ya kashe shi. Duk wata riba ta jahiliyya an soke, amma kuna da uwar kuɗin ku. Kada ku cutar da wani, babu wanda zai cutar

da ku. Ya al'ummata shin na isar da Manzanci? Ya tambayi wannan sau uku. Sai suka ce "E", sai ya ce "Ya Allah Ka shaida" har sau uku. Hadithi Hasan. Sunan Ibn Majah.

Hadith (Za a Rarraba a zama kungiya-kungiya har 73)

Duk da Allah SWT Ya ja kunnen Musulmai da kada su rarraba cikin Ayoyin Alkur'ani, amma cikin IliminSa SWT Ya san sai an rarrabu, shi ya sanya ya tsinkayar da AnnnabinSa domin daɗa ja mana kunne.

Hadithi daga baban Amir al Auzani cewar Mu'awiyya ɗan Abu Sufyan ya tsaya cikinmu yace "Manzon Allah (SAW) ya tsaya cikinmu yace "mutanen da suka gabaceku mazowa littafi (Yahudu da 'Yan Mishan) sun karkasu kashi saba'in da biyu, kuma wannan al'umma (Musulmai) zasu karkasu saba'in da uku, waɗanda saba'in da biyu daga cikinsu duk Wutã zasu shiga, kaso ɗaya ne 'Yan Aljanna. Sune waɗanda basu rarraba ba suke tare da Jama'a. Ibn Yahya da Amr sun ƙara cikin hadithinsu cewar "waɗansu mutane za su bayyana cikin wannan al'ummar tawa, son zuciya da son Jin daɗin duniya zai lulluɓe su, kamar yadda cutar mahaukacin kare wadda bata barin wata jijiya ko ƙashi na maras lafiya face sai ta shigeta"". Sahih daga sunan Abu Dawud.

Ƙarin bayani ga wannan Hadithi

Lallai tabbas, wannan magana ta cikin wannan Hadithi tabbatacciya ce duba ga irin ɗariƙoƙin sufaye da suka baiyana cikin ƙasashen Musulmai a yau a kan doron ƙasar nan. Duk ƙasar da ka je sai ka sami wasu ɗariƙun ɓata da Shehunnai suka ƙirƙirowa kansu da Jahilan mabiyansu wani sabon addini da babu ƙalal-Lahu, babu ƙala Rasulul-Lah sai molon ka.

Hadith (ƙarshen Zamani, alamomin Tashin Ƙiyama).

80. Anas RA ya ce, Manzon Allah SAW ya ce: "Yana daga alamun Tashin Ƙiyama waɗannan abubuwa:

1) Za a ɗauke Ilimin Addinin Musulunci (ta hanyar mutuwar ƙwararrun masu ilimin Addinin.
2) Jahilci (kan Addinin) zai tabbata
3) Shan barasa (giya) zai yawaita (zai zama ba sabon abu ba ne)
4) Zina za ta baiyana a fili. Sahih Bukhari

81. An karƀo daga Anas RA ya ce: Zan faɗa muku wani hadisi wanda babu mai faɗa muku shi bayan Ni. Na ji Manzon Allah SAW yana cewa: "Gabatowar Tashin Ƙiyama akwai waɗannan abubuwa":

1) Ilimi (na Addini) zai yi ƙaranci
2) Jahilci zai yaɗu (ya zama ado)
3) Za a sami yawaitar baiyanar zinace-zinace a fili
4) Mata za su yawaita, maza za su yi ƙaranci ta yadda mata hamsin za su zama cikin ƙarƙashin kulawar mutum namiji ɗaya. Sahih Bukhari.

Komai taƀarƀarewar zamani sai an sami masu bin asalin Musulunci na Gaske ba jabu mai cushe-cushe ba.

372] 232 - (145) An karƀo daga Abu Huraira wanda ya ce, "Manzon Allah SAW ya ce "Musulunci ya fara yana mai baƙo, kuma zai koma (a ƙarshen zamani) yana baƙo, saboda haka kyakkyawan Albishir ga baƙi". Sahih Muslim

374] 233 - (147) An karƀo daga Abu Huraira cewa, Manzon Allah SAW ya ce "Imani zai tattare ya koma Madina kamar yadda maciji yake tattarewa ya koma cikin raminsa". Sahih Muslim

3.7 KAMMALAWA KAN MUSULUNCI.

Wannan shine takaitaccen bayani kan Addinin Musulunci tare da duk wani gargaɗi da busharar da Allah Ya yiwawa Muminai da kuma narkon dake jiran Kafirai Ranar Ƙiyama. Wannan shine Addinin da Annabi SAW ya koyawa Sahabbansa da Matansa da Yaɣansa, kuma suka rayu akai, suka rasu a kai suka koma ga Maliccinsu. Daga cikin Sunnar Manzon Allah SAW, wadda take fassara Alkur'ani aka fitar da SHARI'A da FIQHU waɗanda sune babban jigo cikin aikace-aikacen ADDININ MUSULUNCI, kuma duk wannan a ZAHIRI yake ba a ɓoye ba.

Babu wani abu a ɓoye game da Addini wanda Annabi SAW bai koyawa Sahabbansa ba lokacin da yake a raye tare da su. Alƙur'ani a rubuce yake a baiyane, Sunnar Annabi a rubuce take a baiyane. Wanda ya sani, ya sani, wanda bai sani ba, sai ya koma MAKARANTA.

Babban Ginshikin koyarwar Addinin Musulunci wadda ya zo a cikin Babban Ginshikin Littafin Musulunci watau Alkur'ani, shine TAUHIDI. Domin a Bautawa Allah Shi kaɗai, ba tare da haɗa Shi da wani cikin bautar ba, watau Shirka. Duk Manzanni da suka gabaci Annabi SAW, abinda Allah AWJ Ya aiko su akai kenan. Duk waɗannan bayanan, suna cikin hasken Nassosin Alƙur'ani mai Tsarki tare da fashin baƙin Fiyayyen Halitta cikin Sunnarsa wadda a ka rubuce cikin littattafan hadisai daban-daban.

Sanin TAUHIDI tsantsa (Allah ne kaɗai Mahaliccin kowa da komai, Mai arzuta kowa da komai da ni'imoninSa, kuma Shi kaɗai Ya cancanci a Bauta masa. Sa'annan kowa da komai bawa ne ga Allah kuma dole bawa ya bautawa Allah Shi kaɗai ba tare da shirka ba), shi ke sanya mutum Wadatar zuci da Tawadi'u da Zuhdu. Waɗannan su suke ƙarawa Zuciya Taƙwa, da Ikhlasi cikin aiyukan Ibada tare da Kyautatawa. Muna roƙon ALLAH SWT Taufiƙi.

Sannan babu wani rubutaccen ilimi na Baɗini daga Manzon Allah SAW ko daga Sahabbansa. Kuma duk wanda ya ce Annabi ya taso daga ƙabari ya

ba shi wani abu na addini, ya yiwa Allah da ManzonSa ƙarya kuma abin a titsiye shi ne ya kawo hujja. In ya kasa ko dai ayi masa nasiha ya janye ya koma ga Sunnah, ko in ya ƙi a fille masa kai domin ya daina kawowa Musulmai ruɗu cikin Addinin su.

A dunƙule:

Jalla Jalaluhu cewa yayi:

{ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَتَّبِعُواْ خُطُوَٰتِ ٱلشَّيۡطَٰنِۚ وَمَن يَتَّبِعۡ خُطُوَٰتِ ٱلشَّيۡطَٰنِ فَإِنَّهُۥ يَأۡمُرُ ۞ بِٱلۡفَحۡشَآءِ وَٱلۡمُنكَرِۚ وَلَوۡلَا فَضۡلُ ٱللَّهِ عَلَيۡكُمۡ وَرَحۡمَتُهُۥ مَا زَكَىٰ مِنكُم مِّنۡ أَحَدٍ أَبَدٗا وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ يُزَكِّي مَن يَشَآءُۗ وَٱللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٞ }

Ya ku waɗanda suka yi ĩmãni, kada ku bi hanyõyin Shaiɗan. Kuma wanda ke bin hanyõyin Shaiɗan, to, lalle ne shi, yanã umurni da yin alfãsha da abin da ba a sani ba (na Shirka da zalunci), kuma bã dõmin falalar Allah ba a kanku da rahamarSa, bãbu wani mutum daga gare ku da zai tsarkaka har abada, kuma amma Allah Yanã tsarkake wanda Yake so kuma Allah Mai ji ne, Masani. [Surah An-Nūr: 21]

حُنَفَآءَ لِلَّهِ غَيۡرَ مُشۡرِكِينَ بِهِۦۚ وَمَن يُشۡرِكۡ بِٱللَّهِ فَكَأَنَّمَا خَرَّ مِنَ ٱلسَّمَآءِ فَتَخۡطَفُهُ ٱلطَّيۡرُ أَوۡ تَهۡوِي بِهِ ٱلرِّيحُ فِي مَكَانٖ سَحِيقٖ

Kuna mãsu tsayuwa ga gaskiya dõmin Allah, ba masu yin shirka da Shi ba. Kuma wanda ya yi shirka da Allah, to, yanã kamar abin da ya fãɗo daga sama, sa'an nan tsuntsãye su cafe shi, ko iska ta fãɗa da shi a cikin wani wuri mai nisa. [Surah Al-Ḥajj: 31]

{ وَمَن يَبۡتَغِ غَيۡرَ ٱلۡإِسۡلَٰمِ دِينٗا فَلَن يُقۡبَلَ مِنۡهُ وَهُوَ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ مِنَ ٱلۡخَٰسِرِينَ }

Kuma wanda ya nẽmi wanin Musulunci ya zama addini, to, bã zã a karɓa daga gare shi ba. Kuma shi a Lãhira yana daga cikin mãsu hasãra. [Surah Āli-ʿImrān: 85]

4) ADDININ SUFANCI:

4.1 Shinfiɗa.

Kafin mu shiga cikin babin Sufanci kai tsaye, ina son yi mana tsokaci cikin Tarihin Musulunci zamanin Annabi SAW, da jim kaɗan bayan rasuwarsa SAW, na waɗansu mutane da suka bayyana, kuma suka yi da'awar Annabta. Waɗannan mutanen sune kamar haka:

1) Musailimatul Kazzaab (lokacin Annabi yana raye ya baiyana)

2) Tulaih al-Asadi (bayan rasuwar Annabi ya baiyana)

3) Sajah bint al-Harith (bayan rasuwar Annabi ta baiyana)

Su waɗannan jama'a, ƙarara suka fito suka ce Allah ne Ya turo su da Annabta da kuma Manzanci, kamar yadda Allah SWT Ya turo ManzonSa Muhammad SAW.

Musailimah (Musulmai ne suka ƙanƙastar da sunansa na asali ya koma Musailimah) wanda cikakken sunansa shine Maslamah ibn Habib al Hanafi, ɗan ƙabilar Hanafi wadda ɗaya ce daga cikin manyan ƙabilun larabawa, ya yi da'awar Annabta, ta yadda ya rubutawa Manzon Allah SAW cewa:

Daga Maslamah Manzon Allah zuwa ga Muhammad Manzon Allah, aminci ya tabbata a gareka. Ka sani cewa an bani wani kaso daga cikin wannan al'amari (na Addinin Musulunci), saboda haka, rabin duniya ta mu ce (mu ƙabilar Hanafi), rabin duniya kuma ta Quraishawa (Ƙabilar Manzo Allah SAW), Amma su Quraishawa sun wuce gona da iri (sun keta haddin Allah).

Sai Manzon Allah Muhammad SAW ya mayar masa da amsa kamar haka:

Daga Muhammad Manzon Allah (SAW) zuwa Musailimah al-Kazzaab (mugun maƙaryaci), Aminci ya tabbata ga wanda ya bi Shiriyar Allah, bayan haka, haƙiƙa ƙasa (duniya) ta Allah ce kuma Yana bayar da ita, ga duk wanda Ya ke so cikin bayinSa. Kuma ƙarshen (sakamakon al'amari mai kyau) yana ga masu Taƙwa (tsoron Allah na haƙiƙa).

Musailimah al-Kazzaab ya ƙware cikin rubutun ƙasida da waƙeta, sannan ya ƙware cikin tsafi da surkulle da rufa-ido, ta yadda yake yin abubuwa da suka wuce tunanin wasu jama'a da yawa, har ya ribace tunaninsu suka bi shi cewa akan gaskiya yake. Wannan shi Sufaye a yanzu suke kira Karama. Duk wani Sufiy zaka same shi da yin wani nau'i na tsafi ko surkulle ko rufa-ido da nufin wai Karama ce daga Allah SWT.

Bayan rasuwar Manzon Allah SAW, Musailimah ya tara runduna domin yaƙar Musulmai na Haƙiƙa waɗanda ke kan Tafarkin Manzon Allah SAW.

Shi kuwa Tulaih al-Asadi, bayan Manzon Allah SAW ya rasu sai ya ja zugarsa ta jama'arsa cewa shima Annabi ne. Shima wannan Shaɗanin ya taro runduna domin gamawa da Musulman da suke bayan Manzon Allah SAW.

Itama Sajah bint al-Harith ta ja zugarta cikin da'awarta ta cewa itama Annabiya ce. Ita ce mace ta farko da ta yi da'awar Annabta cikin wannan Al'umma ta Manzon Allah SAW. A lokacin tana da jama'a sun kai dubu huɗu (4,000) waɗanda ta jagora zuwa Madina domin yaƙar Musulman da suke kan Turbar Manzon Allah SAW.

Amma kafin kace kwabo, rundunar Sahabban Manzon Allah SAW ƙarƙashin kwamandan ta, Khaalid bin Walid (zararren takwabin Allah), bisa Khalifancin Dattijon Dattijai baban A'isha, Abubakar as-Siddiƙ, ta murƙushe rundunar Tulaih da Izinin Allah. Ganin an murƙushe Tulaih sai Sajah bint al-Harith ta haɗa kanta da Musailimah kuma ta janye da'awarta ta Annabta ta miƙa

wuya ga Annabcin Musailimah (na ƙarya) wadda shi kuma ya aureta daga baya. Kenan rundunarta ta haɗe da ta Musailimah al Kazzaab. Karawar dakarun Musulunci ƙarƙashin Kwandanta Khalid bin Walid, da na kafirai ƙarƙashin Musailimah, ba da ɓata lokaci ba a kayi fata-fata da rundunar azzalumai ƙarƙashin Musailimah, maƙaryatan Allah da ManzonSa, Annabin Rahama Muhammad SAW. Bayan an kashe Musailimah, an yi nasara akan rundunar Shaiɗanu, sai Sajah bint al-Harith ta komo Musulunci na daidai kuma ta rasu a kan haka.

Kamar yadda Annabi SAW ya rubutawa Musailima, cewar "innal 'Aaƙibata lil Muttaƙiin" ta tabbata. Saboda haka, duk wanda ya ce zai yi faɗa da haƙiƙanin GASKIYA, Wallahi, Tallahi, Billahi sai an yi GALABA a kansa, ko ba a yanzu ba kuwa. Wannan kenan.

Da Sufanci ya fara kafuwa, sai Shehunnansu suka ɗauke hankulan mabiya daga da'awar cewa su Shehunnan sabbin Annabawa ne, a'a, sai suka ce su Waliyai ne amma Waliyan da sun fi Annabawa da Manzanni Daraja gurin Allah AWJ, in ji su. Ko wanene ya yi musu Wahayin hakan? Oho! Suka baiwa kalmar "Wali" wata fassara ta daban domin son zuciya. Za ka fahimci wannan cikin duk rubuce-rubucen su. Wannan ita ce babbar ƙaryarsu ta farko da suka fara shinfiɗawa cikin Addinin Musulunci har suka ribace tunanin wasu jama'ar na Musulmai (masu ƙarancin fahimta) suka mayar da su cikin wani irin Addini na Shirka. Wadda ya canza suna daga Musulunci ya koma Musulmiya - (watau Susulmiya cikin Wutar Jahannama). Ai har zuwa yanzu, ba mu manta da ƙaryar Musailimah al-Kazzaab ba ko? Ya Allah Ka yi mana tsari da Wutar Jahannama.

4.2 Ma'anar Sufiy da Sufanci.

4.2.1 Ma'anar Sufiy a yaren Larabci

An ciro kalmar ne daga suuf watau gashin dabbobin da ake samun ulu (wool a turance). Idan an ce Sufiy ana nufin wanda ya lulluɓe jikinsa da tufafin ulu. Can baya mutane suna canfin duk mai sanya tufafin ulu zai zama mai ilimi. Amma wasu mutanen irin su Al-Biruni suna ganin kalmar Sufiy an laƙanto ta ne daga yaren Girkawa wato Sofos - Ilimi ko hikima. To, koma dai menene za mu iya fahimta nan gaba cewa lallai Sufanci ya fi dacewa da a fassara shi da ***"Kura lulluɓe da fatar ulun Tinkiya".***

4.2.2 Menene Sufanci ko Tasauwuf?

Sufanci wani nau'i ne na Addini (na ƙarya), wanda asalin waɗanda suka fara ƙirƙirar sa, Musulmai ne a zahiri. Sun jingina shi ko sun gwamatsa shi da Musulunci domin ribatar ƙwaƙwalen Musulmai masu ƙaramin sani da fahimta.

Tarihin Musulunci ya nuna cewar babu sufanci cikin ƙarnoni ukun farko na Musulunci. Ƙarnonin da Manzon Allah SAW yace sune mafi alkhairi. Watau har bayan shekaru ɗari uku da kafa Musulunci a bayan ƙasar nan, babu wata hanyar Addini mai suna Tasauwuf ko Sufanci. Koda yake wasu na jingina Ahlus suffah da Sufancin, wannan ba daidai ba ne. domin Ahlus suffah talakawan Sahabbai ne zamanin Manzon Allah SAW, waɗanda suka tare guri ɗaya domin sauraron karantarwar Annabin Rahama shi da kansa, irin su Abu Hurairata.

4.3 Asalin Sufanci

Wanda Tarihi ya tabbatar shine asalin ƙirƙirar Tasauwuf, marubucin mawaƙi ne na ƙasidu kuma mai falsafa. Ya rayu wajen ƙarni na shida zuwa na bakwai (561 – 638) da kafuwar Musulunci. Amma akwai mawaƙa (Asha'irai)

waɗanda suka fara share masa hanya da waƙoƙin zuhdu (gudun duniya) kafin shi. Kamar wata mace mai rubuta ƙasidu, mawaƙiya ɣar Iraq mai suna **Rābi'atul al-'Adawiyya al-Qaysiyya** (Arabic: رابعة العدوية القيسية), ko Rabia Basri. Wai ance ta rayu wajen ƙarni na biyu zuwa na uku da Musulunci. Waƙoƙinta da yawa sun saɓawa ayoyin Alƙur'ani da Sunnar Manzon Allah SAW. Kamar yadda waƙoƙin wasu ɣan ɗariƙar wannan zamani suka saɓawa Alƙur'ani da Hadisan Manzon Allah SAW. Kai wasu kafirci kawai suke tallafawa.

Ga kaɗan daga cikin maganganunta na waƙe:

"Ya Allah idan ina bauta maka ne domin tsoron wutarKa, to Ka ƙona Ni da ita, idan kuma ina bauta maKa ne domin kwaɗayin AljannarKa, to kada Ka saka Ni cikin ɣan Aljanna. Amma idan ina bauta maka ne kawai, saboda Kai kawai, to kada ka hana mini kyawunKa da baya ƙarewa".

Wannan ƙarshen girman kai kenan da nuna isa ga Allah Mahaliccin kowa da komai. Wannan nau'in na addu'a ba a taba samunsa ba daga Manzon Allah SAW ko wani Sahabi.

Sannan wannan matar, ba ta san cewar ba a samun kyawun Allah cikakke da ganin kyawun Allah cikakke, har sai an shiga ALJANNAH. Kuma kyawun Allah na Allah ne kawai, kyawun abinda Allah Ya halitta na abinda Allah Ya halitta ne kawai. Wani kyawun ba ya shiga wani kyawun.

Ga kuma wata maganar tata:

Lokacin da aka tambaye ta "me yasa take yin dubban sujada ta ibada?" Sai ta ce "Bana bukatar wani lada (daga Allah) domin ita (sujadar), Ina yi ne domin Manzon Allah SAW zai (gani) ya yi farin ciki da ita (sujadar). A Ranar Ƙiyama sai yace da ragowar Annabawa ku duba irin (ɗunbun) aikin da wata mace a cikin al'ummata ta gabatar".

Wannan kuma shirka ce. Domin ba a yin aikin Ibada don Annabi shi kaɗai ya gani koda kuwa yana raye ne, domin ba shine zai bayar da lada ko azaba ba. Sannan cewar Annabi zai ce ga ragowar Annabawa "ku duba irin (ɗunbun) aikin da wata mace a cikin al'ummata ta gabatar", wanene ya yi mata Wahayin cewa Annabin zai faɗi hakan? Ko Molon ka ne kawai? Mun tuna cikin shinfiɗa dake bisa nan, matar da ta yi da'awar Annabta ko?

Amma Allah SWT Ya ce:

ٱدۡعُواْ رَبَّكُمۡ تَضَرُّعٗا وَخُفۡيَةًۚ إِنَّهُۥ لَا يُحِبُّ ٱلۡمُعۡتَدِينَ

FASSARA

Ku kirãyi Ubangijinku da ƙanƙan da kai, da kuma a ɓõye: lalle ne Shĩ, bã Yã son mãsu wuce iyãka. [Surah Al-Aʿrāf: 55]

فَٱسۡتَجَبۡنَا لَهُۥ وَوَهَبۡنَا لَهُۥ يَحۡيَىٰ وَأَصۡلَحۡنَا لَهُۥ زَوۡجَهُۥٓۚ إِنَّهُمۡ كَانُواْ يُسَٰرِعُونَ فِي ٱلۡخَيۡرَٰتِ وَيَدۡعُونَنَا رَغَبٗا وَرَهَبٗاۖ وَكَانُواْ لَنَا خَٰشِعِينَ

FASSARA

Sai Muka karɓa masa (Annabi Zakaria) kuma Muka kyautata masa mãtarsa. Lalle ne sũ, sun kasance sunã gudun tsẽre zuwa ga ayyukan alhẽri. Kuma sunã kiran Mu a kan kwaɗayi (ga RahamarMu da jinƙanMu) da fargaba (FushinMu da AzabarMu). Kuma sun kasance mãsu saunar (ƙin) aikata sãɓo gare Mu. [Surah Al-Anbiyāʾ: 90]

Idan har Annnabin Allah AWJ, Annabi Zakariyya da matarsa za su yi kwaɗayi da fargaba gaba ga Allah to waye kuma yake da tabbas idan yayi saɓanin hakan? Koda yake Sufaye sun ce Walinsu kõ Shehunsu yafi Annabi Manzo. Ko waye yayi musu Wahayin hakan? oho.

Saboda haka, ko menene manufarsu ta ɓoye, Sufaye na iƙrarin keɓantuwa domin ibada da zikri ga Allah a baiyane da kuma nuna gudun Duniya, wai

suna kwaikwayon Sahabbai. Amma mu sani, su Sahabbai sun kasance kan Tsoron Allah da Tauhidi tsantsa. Ba sa ƙirƙire-ƙirƙire cikin Addini. Sannan ba su kauce daga kan koyarwar Fiyayyen Halitta shi kaɗai ba.

Babu wani ilimin Baɗini ko Wahdatul Wajudu a lokacin Manzo da Sahabbansa. Idan har Annabi bai koyawa Sahabbansa wannan ba, to waye yake da ikon koya musu da na bayansu a yau? Ya Allah Ka raba mu da ruɗun Shaiɗan la'ananne.

4.4 Ilimin Baɗini

Ilimin Baɗini wanda ya haifar da Wahdatul Wajud da Wahdatush Shahud.

Ilimin Baɗini wanda Sufaye suka ce shine ilimi na haƙiƙa, bai zo ba cikin koyarwar Manzon Allah SAW. Sannan suka ce Ilimin Zahiri na Shari'a wanda Alƙur'ani da Sunnar Manzon Allah SAW ta koyar bai wadata ga mai shi har sai ya haɗa da Ilimin Baɗini. Duniya a birkice kenan, sama a ƙasa, amma ga wasu, kamar Sufaye!

Ibn Arabi wanda cikakken sunansa shine Abû 'Abdullâh Muhammad ibn 'Alî ibn al-'Arabî al-Tâ'î al-Hâtimî (daga ƙabilar Larabawa), ana yi masa laƙabi da Muhyiddeen, wai mai farfaɗo da Addini? Ibn Arabi marubuci ne, ɗan falsafa kuma mawaƙi wanda ya tasirantu da waƙen Rabi'atul 'Adawiyya. Shine farkon wanda ya fara ƙirƙira da tsara Sufanci tare da rubuta shi cikin littafi. Mabiyansa suna ɗaukarsa cewa shi Wali ne - (kafi Annabi).

Yayi da'awar samun wani buɗi (fatahi) ko haske (ilhama / wahayi) daga Allah SWT wanda ya umarce shi da yin wasu abubuwa. Da wannan ne ma ya rubuta wani shahararren littafinsa na Sufanci mai suna 'Futuhaatul Makkati' watau 'Hasken buɗin (ilimi da wahayi) na Makkah'. Saboda lokacin da ya je aikin Hajji wadda ya yi har shekaru uku a Makka, ya fara rubuta littafin. Ai mun tuna da Musailimatul Kazzaab ko?

Ibn Arabi, shine wanda yayi da'awar ya shiga wani tunani har ya gano cewar "Dukkan komai ya samu ne da samuwar abu guda kuma daga gareshi

(jinsinsa) komai ya tsiro kuma wannan abu gudan na farko Shine Allah". Wannan falsafar ita ake kira da **"Wahdatul Wajud"**. Sannan ya ce "Duk abinda ka gani a gabanka wanda ya baiyana, to hoto ne kawai na wancan tushen abu ɗayan na farko watau Allah". Wannan falsafar kuma ita ake kira **"Wahdatush Shahud".** Duk wannan shi ya birkita tunanin wasu Musulman har suke da'awar yanzu sun kai wani matsayin wusuli cikin Zatin Allah SWT, watau sun zama Allah.

Saboda haka, ya tabbata a zahiri game da Sufaye, da'awar sani ko samun ilimin Baɗini (gaibu?) ko wata ilhama mai kama da wahayi, kamar yadda da yawa daga cikin mulhidan da suka gabata suka yi da'awa. Yadda takai mai shi wannan ilimi zai yi wusuli ya narke cikin Zatin Allah? "Wahdatul Wajud". Wa iya zubillahi. A lokacin, su kan ɗauki Shari'ar Allah ta zahiri da ta zo cikin Alƙur'ani da Sunnah su yi watsi da su. Domin yanzu da baɗini suke aiki ba da zahiri ba. A lokacin komai ya halasta har abinda a ka haramta cikin SHARI'A ta ZAHIRI inji su. Luwadi, zina da matan mutane, shan giya, caca, tsafi da surkulle, kai har kisan kai su agurunsu ya halasta.

A yau ɗinnan, Mun san abinda yake gudana duk lokacin wani biki nasu ya zo, ta yadda suke cewa; kayi komai, Shehi ya lamunce maka. Anan za ka ga maza na rungumar mata tare da yin alfasha. Wannan kuwa shine tushen ZINDIKANCI a cikin ISLAMA.

Wannan Baɗini, ba wani abu bane, face irin son zuciyar da ta baibaye mutum, lokacin da ya shiga cikin tunani mai zurfin da ya kai shi ga ruɗewa cikin ƙwaƙwalwarsa. Saboda haka sai ya fassara komai CIKIN SON ZUCIYA da wannan RUƉEWAR tasa, domin ya fita daga haiyacinsa koda kuwa na wani ƙanƙanin lokaci ne. A lokacin ya zama ZINDIKI FASIKI MAƘARYACI kuma MAHAUKACI.

4.5 Ginshiƙan Sufanci:

1) Tsoron Allah da gudun duniya (suna riyawar hakan). Saboda a hankali za ka fahimci ƙarya su ke yi.

2) Keɓancewa (shiga halwa) domin tunani da Zikri. Zikirin da suka ƙirƙiro tare da kaifiyyar yin sa, cikin masallatai da zaawiyyarsu. Ana rawa da kade-kade har da tsalle da majajjawa wasu lokutan.

3) Ƙirƙira ko Jingina da wata ɗariƙa domin saduwa da Muƙaddami (dole wani muƙaddami yayi maka tsani, kuma dole sai ta hanyar Ɗariƙa).

4) Yarda da bin wasu aikin ibada sabi waɗanda Waliyin ko Shehun ɗariƙar ya ƙago, ɗoriya kan koyarwar Manzon Allah SAW.

5) Yarda da ziyarar maƙabartu tare dayin bauta ciki ga Shehunnai da Waliyyai. (Wannan shirka ce)

6) Yarda da cewar Annabawa da Waliyai da Shehunnai ke juya akalar duniya na arzutawa da talautawa. Duk abinda kake da shi na arziki ko lafiya ko yaya, to Shehi ne ko Wali ko Annabi ya baka, ba Allah ba. (Ƙarya ce, Allah ne kawai Mai arzutawa Mai talautawa Mai rayawa Mai kashewa).

7) Yarda da cewar Wali ko Annabi zai iya tashi bayan ya mutu har ya bayar da wata ibada. (Wannan ƙarya ce. Kullu nafsin zaa'iƙatul maut). Ina jin dai kasan mecece mutuwa koda baka mutu ba a yanzu.

8) Yarda da ƙarerayi waɗanda babu hujja ko ƙanƙani a kai. Ƙarerayin da basu sami goyon bayan Alƙur'ni ko Hadisan Manzon Allah SAW ba.

9) Hana Tambayar dalili ko hujja ga Shehu ko Wali, akan duk abinda ya aikata ko ya umarci muridi da ya aikata. Kuma dole ka kasance kamar gawa gaban mai wanke ta duk lokacin da ka je gaban Shehi ko wani Wali.

10) Barrantuwa da duk wata ɗariƙa da Shehun ɗarikar da ba ta mutum ba. Watau duk wata ɗariƙa tare da Walinta ko Shehinta ƙarya ce, sai tasa ita kaɗai, ita ce gaske.

11) A ƙarshen ƙarshe, Sufiy muridi, ya kai ga magaryar tuƙewa ya zama Allah (Wahdatul Wajud), domin Walinsa da Shehunsa duk Alloli ne. Waiyazubillahi. Daga lokacin komai na zunubi, ya halasta a gare shi. Idan yayi wani aikin Ibada kamar Sallah da Azumi, to na ganin ido ne, amma a zuci ba don Allah yayi ba, sai don gudun kada ragowar Musulmai na gari su zarge shi, kuma dai domin ya zama Allah a yanzu. Allah zai bautawa Allah ne? Wannan shi ake kira Zindikanci orijinal kuma lamba wan.

Annabin Rahama bai taɓa koyar da wannan ba har ya bar Duniya. Hasali ma abinda yafi so shine a kiraye shi 'Bawa Manzo'. Haka Sahabbansa da Matansa, ba su taɓa sanin wannan Ruɗanin ba, na Bawa ya zama Allah, Allah kuma ya zama Bawa. Can da ƙazantar Mushrikai.

4.6 Sunayen kaɗan daga cikin Manyan Sufaye da taƙaitaccen tarihin wasu.

4.6.1 Ibn 'Arabi

Haihuwarsa 561 AH mutuwarsa 638 AH = 1165/1240 miladiiiiyya. Mabiyansa na kiransa da Muhyiddeen, Ash-Sheikhul Akbar, saboda yawan iliminsa (na ruɗani), saboda duk ilimi kan Addini koma bayan na Manzon Allah SAW ruɗu ne. Shine farkon wanda ya ƙirƙiro Sufancin da ragowar Sufaye suka ɗosana. Sunan ɗariƙarsa **Akbariyya,** wadda babban reshenta yana Cairo (Alƙahira). Shi ma ya yi da'awar duk Rubutunsa Saukakke ne. To amma daga wa zuwa wa. Idan har yana da'awar Allahntaka. Shine farkon wanda ya ƙirƙiri Ilimin Baɗini watau Ilimin Haƙiƙa wanda ya haifar da Wahdatul Wajud da Wahdatush Shahud, kamar yadda ya gabata a nan sama.

4.6.2 Sayyed Badiuddin

Ai daga jin sunan Badi'uddeen mai ƙagar Addini, kasan an kauce daga Islama. Shine ya ƙirƙiri ɗariƙar **Madariyya** Silsila ɗan ƙasar Syria kuma an haife shi a Aleppo. Daga aikin Hajji sai ya wuce India kuma a can ne ya ƙirƙirar da ɗariƙarsa.

4.6.3 Al-Ghazālī

Haihuwarsa a1058 mutuwarsa a 1111, malamin lissafi, ɗan falsafa kuma Sufiy sannan Alƙali Faqihi, mabiyansa sun ɗauke shi Mujaddadi cikin Islam wanda ake samu duk bayan Shekaru ɗari kuma suna kiran shi Burhanuddeen. Asali yana bin Mazhabar Shafi'i ne. Yana da littattafai irin su Ihya'u 'Ulumuddeen (Farfaɗowar Ilimi) da Tahaafutal Falasifa (cin karon masu falsafa).

4.6.4 **Shaykh Abdul Qadir Gilani**

Haihuwarsa a 1077 mutuwarsa a 1166, Sufi kuma masanin Fiqh ne cikin Mazhabar Hambali. An haife shi a Na'if gabas da Baghdad. Malaminsa cikin sufanci shine Abu'l-Khair Hammad ibn Muslim al-Dabbas. Yakan koyar da Tafsir da Hadith da safe sannan da yamma ya koyar da ilimai kan zuciya da dangogin sha'awa. Shine wanda ya ƙagi ɗariƙar **Ƙadiriyya**.

4.6.5 **Abul Hasan ash-Shadhili**

Ya mutu shekara ta 1258. Shine ya ƙago Ɗariƙar **Shaziliyya** tare da Zikri a fili mai ƙarfi saɓanin a hankali ba tare da baiyanawa ba, kamar yadda ya zo cikin Alƙur'ani mai Tsarki. Ragowar ɗariƙun Sufaye na koyar da zuhdu da haƙuri (Ɗariƙu-Sabru) amma shi ɗan tamore ne mai umartar mabiyansa da kada su taɓa barin duk abinda ba a haramta ba amma dai su zama masu godiya (Ɗariƙush-shukru). Abul Hassan ash-shazali ya ce yayi mafarki cewar Manzon Allah SAW ya ba shi Hizb Bahr, wani wurudi da Shazali ya

harhaɗa da ayoyin Alƙurr'ani da Addu'o'in da suka zo cikin Sunnar Manzon Allah SAW. Kuma ya rantse da Allah cewar bai karanta wannan wurudin ba, face kamar yadda Annabi SAW ya karantar da shi a mafarkin. (Ƙarya zunzurutu, mafarki, mafarki, mafarki, ƙarerayin ɗariƙun Sufaye domin jan hankali masu ƙarancin ilimi).

4.6.6 Baha-uddin Naqsh-band

Haihuwarsa a 1318 mutuwarsa a 1389, babban Sufi ne wanda aka haifa a ƙasar Bukhara Uzbekistan (Allahu Akbar, ka ji ƙasar su ɗaya da Imam Bukhari mai Sahihul Bukhari). Duniya kenan, idan wani ya kauce to wani yana kan daidai har abada. Bahauddin Shine ya ƙirƙiri ɗariƙar **Naqshbandiyya**. Ance Koyarwarsa ta ƙunshi Alƙur'ani da Sunnah. Tambayar anan me yasa sai ya ƙirƙirar da ɗariƙa zai koyar? Ance yayi ƙoƙarin samar da daidaito tsakanin tarbiyya ta Ruhi da harkokin rayuwar Duniya ta yau da gobe a zamanin sa.

4.6.7 Abū al-‘Abbās Ahmad ibn Muhammad at-Tijāniyy ko Ahmed Tijani

Haihuwarsa a 1735 mutuwarsa a 1815, an haife shi a Algeriya kuma shine ya ƙirƙiri ɗariƙar **Tijjaniyya.** Lokacin da yakai shekaru sha shida mahaifan sa duka biyun sun rasu. A lokacin ya yi aure sannan ya ci gaba da neman ilimi cikin bin malaman ɗariƙoƙin Ƙadiriyya da ɗariƙar Ahmad al-Habibi b. Muhammad. Sa'ad da ya je garin Fez sai ya haɗu da wani ɗan duba wanda ya ce masa zai zama wani gawurtaccen mai Fatahi (wanda aka yi masa ilhama ko wahayi). A shekarar 1772, sai ya tafi Makka domin yin aikin Hajji da neman ilimin Sufanci. A wannan lokacin ya haɗu da manyan wasu Shehunnan na ɗariƙar Khalwati da Samaniyya, inda ya karɓi ɗariƙarsu.

Yana cikin wannan hali na koyar da ɗariƙun da yake ciki, kwatsam sai ya yi da'awar cewar ya sami wahayi daga Manzon Allah SAW cewa ya ja zugar tafiyarsa ta kansa. Shi yasa a shekarar 1781, ya ƙirƙiro ɗariƙar Tijjaniyya

kuma ya yi watsi da ragowar ɗariƙun da yake kai a da. Musailimah al-Kazzaab yana samun mataimaka.

Tijjani ya baiwa kansa Hatimin Walittaka, sannan mabiyansa sun bashi Hatimin Walittaka, lokacin da ya tumbatsa ya ce:

"Albarkatun da suke kwararowa daga Manzon Allah SAW (mu fahimta anan, ba daga Allah ba) waɗanda suke kamanceceniya da Annabawa ne kawai ke karɓar su. Duk kuma abinda ya gudana ya bijiro cikin kamanceceniya ta Annabawa to kama ta ce take karɓarsa (watau yanzu ya zama Annabi a fakaice). Kuma daga gareni ne ake rabawa ga dukkan halittu tun daga farkon Duniya har zuwa busar ƙahon (Tashin Ƙiyama). Babu wani Wali da zai sha ruwa ko ya shayar da wani mutum ruwa, face daga Tafkinmu tun daga farkon Duniya har zuwa busar ƙaho. Ran Annabi da rai na kamar haka suke, sai yayi nuni da yatsunsa biyu, na tsakiya da manuniya. Ran Annabi yana taimakon Annabawa da Manzannin, rai na yana taimakon duk wanda yake gabas da yamma da masu haƙuri da Waliyyai tun kamin fara halitta har zuwa abada, (Minal azal ila abad). Waɗannan ƙafofi biyun nawa suna kan wuyan duk wani Wali tun daga lokacin Adam har zuwa busar ƙaho. Matsayinmu a gurin Allah ranar Kiyama babu wanda zai kai gareshi cikin dukkan Waliyai, kai babu ma wanda ya isa ya kusance shi, komai girmansa kuma komai ƙanƙantarsa. Kai dukkan Waliyai tun daga farkon halitta har zuwa busar ƙaho babu wanda zai kai ga matsayina". In ji Ahmad Tijjani mai Ɗariƙar Tijjaniyya.

Kunga can baya yana cewa “mu” domin fakewa da Annabi, amma a ƙarshe sai yace “matsayina”. Kenan har Annabin bai kai matsayinsa ba.

Wannan shine babban girman kai na ƙarshe da wulaƙanta ragowar Waliyan Allah salihan bayi. Duk duniya babu wani Wali wanda Walittakarsa takai Walittakar Annabawa da Manzanni da Shuhada'a da Siddiƙai da Salihan bayi. Amma sai ga wani Mushriki yana wulaƙanta su, wai digadigansa biyu suna kan wuyan waɗannan bayin Allah na gari wanda har da Annabin da yake da'awar bi cikinsu. Allah Ya isa.

Anan sai mu tambayi Tijjani, wanene ya yi masa Wahayin waɗannan kalaman? Allah ko Annabi ko Mala'ika? Hasbunallahu wa ni'imal wakiiil. Kuma wai duk da sunan Musulunci. Ya manta mun karanta cikin Alƙur'ani cewar babu sauran saƙo an riga an kammala mana Addininmu ta bakin da baya ƙarya, bakin Manzon Allah SAW.

Tijjani ya rubuta Littattafai da yawa amma mafi shahara shine Jawahirul Ma'ani, inda ya ringa sukuwa har da zamiya ta ƙarerayi....

- A ciki ya ce in ka ganshi kaga Annabi kuma kaga Allah.

- Annabi ne ya bashi salatul fatih ƙiri da muzu, bayan sama da shekaru dubu da rasuwar Manzon Allah SAW.

- Ladan karanta salatul fatih ɗaya daidai yake da ladan karanta Alƙur'ani daga Baƙara zuwa Naasi sau dubu shida.

Da sauran ƙarerayi waɗanda basu sami wani goyon bayan Alƙur'ani ko Hadisi ba.

Don Allah, ta ina wanda ya san ma'anonin Alƙur'ani da Hadisan Manzon Allah SAW zai yarda da wannan Tatsuniyar Gizo da Ƙoƙi dake cikin Jawahirul Ma'aani?

Ya Allah Ka kiyaye mu daga sharrin SUFAYE!

4.6.8 Ibrāhīm Niasse (Nyass)

Haihuwarsa a 1900 da mutuwarsa a 1975, ɗan ƙabilar Wolof ne, mabiyansa suna yi masa laƙabi da Sheikhul Islaam. Babban Sufiy kuma babban shugaban ɗariƙar Tijjaniyya a Senegal. An haife shi a shekara ta 1900 miladiyya a wani ƙauye mai suna Tayba Naseen dake tsakanin garin Kaolack (Kaulaha) da bodar ƙasar Gambia.

Mahaifinsa Alhaji Abdullahi Nyass (1840-1922) shine babban Muƙaddamin ɗariƙar Tijjaniya a yankin Saalum, a farƙon ƙarni na ashirin miladiyya. Lokacin da Ibrahim yana ƙarami sai mahaifinsa ya ɗauko shi suka koma garin Kaulaha, inna suka ƙirƙiri zawiyyar Liyuna Naseen. Bayan rasuwar mahaifinsa a shekarar 1922, sai babban yayan Ibrahim mai suna Muhammad ya zama Khalifan mahaifinsu.

Lokacin da Sheikh Ibrahim yakai shekaru 22 ya kasance mai aikin noma cikin gonakin su na gado, tare da koyar da matasa ɗariƙar mahaifinsa wadda ya gada. Waɗannan matasa da ragowar manyan gari sai yawansu ya ringa ƙaruwa ya haɓaka a wani gari mai suna Kosi Mbiteyin kusa da garin Kaulaha. Duk da cewa Ibrahim bai ce shine khalifan mahaifinsu ba saboda babban yayansa, amma yadda mabiyan Ibrahim suka haɓaka, sai rikici ya ringa ɓarkewa tsakanin mabiyan ɓangarorin biyu, na shi, da na wansa Muhammad.

A shekara ta 1929, lokacin da Ibrahim yake cikin gona a garin Kosi Mbiteyin, sai kawai ya yi da'awar **an bashi mukullin asarar ɗin Ilimin Ubangiji** saboda haka yanzu shine babban Khalifan Sufiy Sheikh Ahmadu Tijjani mai ɗariƙar Tijjaniyya, wanda wannan matsayin babu wanda ya kai gareshi a daidai wannan lokacin. A lokacin ne Sheikh Ibrahim ya kafa dokar cewar duk wanda yake son ya kai ga mataki na ma'arifa (sanin ilimin Haƙiƙa) a cikin ɗariƙar Tijjaniyya, sai ya bi ta hannunsa.

A shekara ta 1930 bayan Sallar Idin Ƙaramar Sallah sai faɗa ya ɓarke tsakanin mabiyan Sheikh Ibrahim da na yayansa Muhammad. Wannan hayaniya ta sa Ibrahim ya yi ƙaura da mutanensa zuwa wani sabon gurin. A yammacin wannan yinin, sai Ibrahim ya fita tare da yan tsirarun muridansa mafi kusanci da shi, domin neman sabon gurin da za su zauna domin ci gaba da da'awarsa ta Annabta? ko Walittaka? Washe gari sai suka ƙaddamar da zawiyyarsu a garin Madina Bai'i, wani ɗan ƙauye kusa da garin Kaulaha wanda daga baya garin Kaulahan ya haɗiye shi.

A shekara ta 1945 Ibrahim ya koma garinsa na haihuwa inda ya sake gina gidansu bayan gobara ta ƙone shi, kuma ya zama Khalifan mahaifinsa da Tijjani. A nan ban sami tarihin me ya sami yayansa Muhammad ba.

Sheikh Ibrahim ya yi tafiye-tafiye tsakanin shekarun 1930 da 1940 domin neman mabiya, kuma ya samu tun daga kan ƙasashen Afrika ta Arewa inda ɗariƙar Tijjaniyyar ta samo asali, har zuwa nan Afrika ta yamna. Lokacin da ya je aikin Hajji a shekara ta 1937, ya haɗu da mai martaba Sarkin Kano Abdullahi Bayero wanda ya yi masa mubaya'ar zama Sufiy cikin ɗariƙar Tijjaniyya. Wannan ta sa da ya je Kano ya samu mabiya masu ɗinbin yawa.

A lokacinsa ne wani ɓangare na ɗariƙar Tijjaniyya mai suna Faira ya samu kafuwa da gindin zama. Duk wannan ya tsiro ne daga koyarwar Tijjani da Ibrahim Inyass ta hanyar littattafan su musamman Jawahirul Ma'aani, wanda a yanzu saboda Ilimin Kitabu da Sunnah yana yaɗuwa kamar wutar daji, masu wancan littafin suke ɓoye shi tare da hana karantashi a bainar jama'a. Amma ina, Hasken Rana, tafin Hannu bai iya Karewa.

Kafin mutuwarsa Inyass ya rubuta littattafai da yawa na Sufanci kuma ya zo nan Kano lokacin da abubuwan da suka faru suka faru, na ƙazantar koyarwar ɗariƙar Tijjaniyya, waɗanda baiyana su anan bai kamata ba saboda munin ƙazantarsu.

A shekara ta 1975 miladiyya, Ibrahim Inyass ya kamu da rashin lafiyar ruɓewar ɓarin jikinsa ta yadda ya ringa ɗoyi. Yayi ƙoƙarin ya tuba ya nunawa muridansa cewa, akan ɓata suke sakamakon watakila wa'azantuwa da yayi da wannan rashin lafiyar, amma suka hanashi tuba cewar akan daidai suke kuma za su tsaya masa gaba ga Allah su ba shi kariya Ranar Hisabi. Yadda ya yaudare su haka suka yaudare shi. Kama tu dinu tu dana. Lokacin da gargara ta zo masa, masu jinyarsa sun ji yana cewa minti biyar, minti biyar. Daga nan bai sake furta wata kalma ba rai yayi halinsa.

Daga cikin irin mabiya Sufaye irin su Inyasi, na ji wani muridinsu yana cewa "idan kana buƙatar agajin gaggawa Shehu za ka kira, domin matsayinka bai kai ka kirawo Allah kai tsaye ba. Idan ka kirawo Shehi, shi kuma sai ya yi

kiran Allah sai buƙatar ka ta biya. Wannan kuma babbar AƘIDAR su ce, na cewar Waliyan su da Shehunnan su, suna da tasiri kan Allah SWT. Watau zasu iya juya Allah ya yi abinda suke so yayi. Na'uzu bilLahi min zaalik.

Don Allah menene banbanci waɗannan mutanen da Mushrikan Makka kafin zuwan Annabi Muhammad SAW da Addinin Musulunci?

Suma cewa suke yi a kira Lata da 'Uzza da Manata, ba Allah kai tsaye ba. Lata da 'Uzza da Manata Salihan bayin Allah ne da suka gabata. Kuma wannan Aƙida ta Shirka, da ragowar kafirci, Manzon Allah SAW ya yaƙa cikin shekaru ashirin da uku na Annabtarsa.

Sai Gashi yanzu ana mayar da Al'ummar Musulmai cikinta. Allah Ya isa.

Jan hankali

Wannan kuwa izina ce ga muridansa da ragowar magoya bayansa. Kuma wannan yanayin mutuwarsa, yayi kama da lokacin da mutuwa ta zowa Fir'auna. Inda Fir'auna ya ce yayi Imani da Allahn Banu Isra'ila. Amma inaa! Allah Ya ce, sai yanzu (da ka ga mutuwa miraran). La'alla minti biyar da Inyass yake faɗa, na ayi masa jinkiri ne ya tuba, amma aka ƙiya, domin me?

Allah AWJ Ya ce cikin Alƙur'ani mai Tsarki:

وَلَوۡ يُؤَاخِذُ ٱللَّهُ ٱلنَّاسَ بِظُلۡمِهِم مَّا تَرَكَ عَلَيۡهَا مِن دَآبَّةٖ وَلَٰكِن يُؤَخِّرُهُمۡ إِلَىٰٓ أَجَلٖ مُّسَمًّىۖ فَإِذَا جَآءَ أَجَلُهُمۡ لَا يَسۡتَـٔۡخِرُونَ سَاعَةٗ وَلَا يَسۡتَقۡدِمُونَ

FASSARA

Kuma dã Allah Yanã kãma mutãne da zãluncinsu, dã bai bar wata dabba ba a kan ƙasa. Kuma amma Yanã jinkirta musu zuwa ga ajali ambatacce. Sa'an nan idan ajalinsu ya zo, bã zã a yi musu jinkiri ba kõ da sa'a guda, kuma bã zã su gabãta ba. [Surah An-Naḥl: 61]

لِيَحۡمِلُوٓاْ أَوۡزَارَهُمۡ كَامِلَةٗ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ وَمِنۡ أَوۡزَارِ ٱلَّذِينَ يُضِلُّونَهُم بِغَيۡرِ عِلۡمٍۗ أَلَا سَآءَ مَا يَزِرُونَ

FASSARA

Dõmin su ɗauki zunubansu cikakku a Rãnar Ƙiyãma, da kuma zunuban waɗanda suke ɓatarwa bã da wani ilmi ba. To, abin da suke ɗauka na zunubi ya mũnana. [Surah An-Naḥl: 25]

Hadith.

Manzon Allah SAW ya ce ana karɓar tuban mutum matuƙar bai kai ga gargara ba. Ya Allah Ka tsaremu daga Taɓewa.

A ƙarshe Allah SWT cewa ya yi:

وَإِذَا سَأَلَكَ عِبَادِي عَنِّي فَإِنِّي قَرِيبٌۖ أُجِيبُ دَعۡوَةَ ٱلدَّاعِ إِذَا دَعَانِۖ فَلۡيَسۡتَجِيبُواْ لِي وَلۡيُؤۡمِنُواْ بِي لَعَلَّهُمۡ يَرۡشُدُونَ

Kuma idan bãyiNa suka tambaye ka daga gare Ni, to, lalle Ni Makusanci ne. Ina karɓa kiran mai kira idan ya kirã Ni. Sabõda haka su nẽmi karɓawaTa, kuma su yi ĩmãni da Ni: tsammãninsu, su shiryu. [Surah Al-Baqarah: 186]

Saboda haka, kowa Allah zai kira kai tsaye (cikin kowanne hali) ba tare da wata wasiɗa (tsakani) ba. Kuma kiran Wali ko Shehi Shirka ne kuma Kafirci ne, ka yarda ko kar ka yarda wannan kai ta shafa, mu hakkin gaya maka Gaskiya ya sauka daga kanmu.

4.6.9 Sheikh Ɗahiru Usman Bauchi.

(Haihuwarsa 29 Yuni 1927), Ɗahiru Bauchi ya kasance babban Sufiy kuma babban Khalifan Tijjani cikin ɗariƙar Tijjaniyya a Nijeriya.

Ɗahiru Bauchi babban mai yarda da goyon bayan ɗariƙar Tijjaniyya ne a Nijeriya tare da bata kariya cikin duk koyarwarta cikin Jawahirul Ma'aani. Yayi gaba ko kuma in ce yana gaba da masu karantar da Tauhidi irin su Ash-Sheikh Abubakar Mahmoud Gumi da Ash-Sheikh Abdul'Aziz Dutsen Tanshi da ragowar Ahlus Sunnah dake cikin Nijeriya. Ya ce da ka zaɓi Musulmi Ahlussunnah ga shugabanci gwara ka zaɓi wanda ba Musulmi ba ya shugabance ka.

Na ji da kunnena yana bayar da fatawar cewar Manzon Allah SAW ya fito ƙarara ya baiwa Tijjani Salatul Fatih, babu wata wasiƈa shi-da-shi kuma a farke ba cikin bacci ba, bayan shekara sama da dubu da rasuwar Manzon Allah SAW. [Wanga gundumemiyar ƙaryata shi ka faɗi].

Allah JJH Ya cewa ManzonSa SAW:

إِنَّكَ مَيِّتٌ وَإِنَّهُم مَّيِّتُونَ

FASSARA

Lalle kai (Ya RasululLah) mai mutuwa ne, kuma su mã lalle mãsu mutuwa ne. [Surah Az-Zumar: 30].

Tabbas Manzon Allah SAW ya rasu kuma duk cikin Alƙur'ani da Hadisan Manzon Allah SAW babu inda akayi tsokacin Annabi zai fito daga ƙabari, domin ya baiwa wani Wali ko Shehi, wani abu wala a zahiri wala a mafarki.

Rigingimu da yawa sun faru tsakanin Sahabbai a ƙarnin farko na Musulunci, ƙarnin da Manzon Allah SAW ya ce shine ƙarnin da yafi Alkhairi har zuwa Tashin Ƙiyama, amma bai fito daga ƙabari ya sasanta su ya ce ga yadda za a yi - ga yadda za a yi ba, wala a zahiri wala a mafarki. Sai yanzu ne zai fito cikin jagwalgwalallen ƙarni ya ba da wani abu? Ƙaryar banza kawai, maha'inta.

Sannan na ji da kunne na, ɗaya daga cikin manyan muridan Ɗahiru Bauchi yana cewa duk abinda ka gani a gare shi, to Annabi ne ya ba shi. Duk wannan haka suke yaɗa shi cikin kafafen sadarwa na zamani.

Allah SWT Ya ce:

وَمَا بِكُم مِّن نِّعۡمَةٖ فَمِنَ ٱللَّهِۖ ثُمَّ إِذَا مَسَّكُمُ ٱلضُّرُّ فَإِلَيۡهِ تَجۡـَٔرُونَ

FASSARA

Kuma abin da yake a gare ku na ni'ima, to, daga Allah ne. Sa'an nan kuma idan cũta ta shãfeku, to, zuwa gare Shi kuke hargõwa (neman taimako). [Surah An-Naḥl: 53]

ثُمَّ إِذَا كَشَفَ ٱلضُّرَّ عَنكُمۡ إِذَا فَرِيقٞ مِّنكُم بِرَبِّهِمۡ يُشۡرِكُونَ

FASSARA

Sa'an nan idan Ya kuranye cũtar daga gare ku, sai gã wani ɓangare daga gare ku game da Ubangijin su sunã shirka. [Surah An-Naḥl: 54]

Jan hankali

Ina mai nasiha da jan hankalin babban tsohon Sufiy na Bauchi, kafin rai yayi halinsa, idan har Allah Ya sa wannan littafi ya kai gareshi:

وَٱللَّهُ خَلَقَكُمۡ ثُمَّ يَتَوَفَّىٰكُمۡۚ وَمِنكُم مَّن يُرَدُّ إِلَىٰٓ أَرۡذَلِ ٱلۡعُمُرِ لِكَيۡ لَا يَعۡلَمَ بَعۡدَ عِلۡمٖ شَيۡـًٔاۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمٞ قَدِيرٞ

FASSARA

Kuma Allah ne Ya halicce ku, sa'an nan Yanã kaɾɓar rãyukanku, kuma daga gare ku akwai wanda ake mayarwã zuwa ga mafi ƙasƙancin rãyuwa (tsoho

tukub), dõmin kada ya san kõme a bãyan dã ya zama mai ilmi. Lalle Allah ne Masani Mai ĩkon yi. [Surah An-Naḥl: 70]

Kafin rikirkicewar tsufa ta daɗa cimmasa, lokacin da zai rasa kansa, shin a duniya yake ko a lahira, lokacin da zai fara shiga gargara, da ya tuba ya yiwa yayan sa da jikokin sa da mabiyan sa, nasihar gaskiya kan abinda da aka ruɗe shi, shi kuma ya ɗora su akai. Kada ya yi mutuwar Fir'auna da Inyass.

وَمَنۡ أَضَلُّ مِمَّنِ ٱتَّبَعَ هَوَىٰهُ بِغَيۡرِ هُدٗى مِّنَ ٱللَّهِۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهۡدِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلظَّٰلِمِينَ

".....kuma wãne ne mafi ɓata daga wanda ya bi son zuciyarsa, bã tãre da wata shiriya daga Allah ba? Lalle ne, Allah bã ya shiryar da mutãne azzãlumai". [Surah Al-Qaṣaṣ: 50]

4.6.10 Sarkin Kano Sanusi Lamido Sanusi

(Haihuwarsa 1961). Farkon da'awarsa yana cikin ƙungiyar 'Muslim Brothers' wadda shugaban ta ɗan Shi'a ne. Sarkin Kano Sanusi na biyu Sufiy ne ɗan boko kuma shine babban Shugaban Sufayen ɗariƙar Tijjaniyya a Nijeriya a daidai wannan lokacin. Muna sauraron shi kuma wacce irin **ƙaryar zai guntso ya feso mana!** Amma dai ya sani, Allah SWT Ya ce:

إِنَّمَا يَفۡتَرِي ٱلۡكَذِبَ ٱلَّذِينَ لَا يُؤۡمِنُونَ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡكَٰذِبُونَ

Abin sani kawai waɗanda bã su yin ĩmãni da ãyõyin Allah, sũ ne suke ƙirƙira ƙarya. Kuma waɗannan sũ ne maƙaryata. [Surah An-Naḥl: 105]

Haba malam, mutane ba imani ba tsoron Allah ba jin kunyar Allah da Manzon Allah SAW. Ƙaryar yau da ban, ta gobe da ban duk cikin wannan Addini namu na Musulunci. Babu Aya babu Hadisi, mutum ya ringa zaƙalƙalewa kai ka ce Ubansa aka saukarwar da Alƙur'ani - Alƙur'anin da bai gama sanin ma'anoninsa ba ballantana ya yi Imani tare da aiki da shi.

Ina faɗin Kalmarku ta {LA'ILAHA ILLALLAHU - MUHAMMADUR RASULULLAHI SAW}. Ko baku fahimceta ba ne? Amma ba komai Allah SWT Yana nan a Madakata.

4.7 Yankorensu

Kasancewar Sufanci yayi kama da waɗansu addinai na maguzanci na wajejen ƙasashen Asia da Turai, shi ya sanya jama'ar da ba Musulmai ba a waɗannan ƙasashen suke ganin Sufanci addini ne da zai iya karɓuwa da kuma cakuɗuwa da ragowar addinai ba tare da nuna banbanci ko ƙyamar su ba. Shi ya sanya za ka ji Turawa suna yabon su da cewar sune Musulmai na gari. Saboda aƙidarsu ta kusa zuwa ɗaya - kaɗe-kaɗe, raye-raye, waƙe-waƙe, shaye-shaye, bushe-bushe, munafunce-munafunce da sauran aikin baɗala.

Duk da haka wasu Turawan, bayan nazari akan haƙiƙanin Musuluncin da Annabi SAW ya zo da shi da kuma irin abin da Sufaye suka saɓa da shi, sai suka ce lallai Sufanci addinine mai zaman kansa.

Masu bincike cikinsu (Turawan) suka ce dalilin kafuwar Sufanci shine domin dakushe kaifin bazuwar Musulunci na Haƙiƙa. Wannan kuwa zai iya zama gaske - cewar a samawa Musulunci kishiya a cikinsa domin kada su zauna lafiya. Kuma wanna batu tabbatacce ne ta yadda duk wani ɗan ɗariƙa faɗa yake yi da duk wanda yace abi Alƙur'ani da Sunnar Fiyayyen Halitta, kuma ayi watsi da duk wata aƙida da koyarwar da ba ta sami asali ba daga Manzon Allah SAW da Sahabbansa.

Biri yayi kama da mutum idan muka yi la'akari da shaidar wani Pastor a da, wanda CAN ta tura su ƙasashen Larabawa da nufin koyan larabci da sanin Addinin Musulunci, ta yadda idan sun dawo nan gida Nijeriya, su yi shigar bultu domin rikirkita Musulunci da Musulmi.

Amma shi Allah Ya taimake shi domin ya fahimci ashe Musulunci shine Addinin Gaskiya, saboda haka a yanzun in dai ba ya rasu ba, to cikin da'awa yake domin ɗaukaka Kalmar Allah cikin Musulunci. Wannan dattijo kuwa shine Professor Dr. Dawud Ujobi mutumin Benue State.

Dr. Ujobi yace fadar Paparoma ce da ɗauki nauyin buga Jawahirul Ma'aani kundin yan ɗariƙar Tijjani. Ya ce shi, ya ganshi a cikin 'archives' a cikin ɗakin tara littattafai dake can Vatican, kuma har da sunayen waɗanda aka sanya suka yi wannan aikin tun can shekaru masu yawa a baya. Duk waɗannan bayanai za ka iya samun su a kafafen sadarwa na zumunta dake kan yanar gizo. Kenan Sufaye suna da iyayen gida ta ƙarƙashin ƙasa. E, labarin dambarwar da aka yi tsakanin Muhammadu Marwa Maitatsine da Sarkin Kano Sunusi na ɗaya, na wancan lokacin sirri ne buɗaɗɗe.

Koma dai menene, abinda za mu faɗa kawai shine, kamar yadda Allah Ya faɗa ne cikin LittafinSa mai Tsarki JWA:

وَإِذْ يَمْكُرُ بِكَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ لِيُثْبِتُوكَ أَوْ يَقْتُلُوكَ أَوْ يُخْرِجُوكَ ۚ وَيَمْكُرُونَ وَيَمْكُرُ ٱللَّهُ ۖ وَٱللَّهُ خَيْرُ ٱلْمَٰكِرِينَ

Kuma a lõkacin da waɗanda suka kãfirta sukẽ yin mãkirci game da kai, dõmin su dakatar da kai (hanaka yin da'awa), kõ kuwa su kashe ka, kõ kuwa su fitar da kai, sunã mãkirci kuma Allah Yanã mayar musu da mãkirci kuma Allah ne Mafificin mãsu (mayar da) mãkirci (akan azzalumai, kafirai). [Surah Al-Anfāl: 30]

ٱتَّخَذُوٓا۟ أَحْبَارَهُمْ وَرُهْبَٰنَهُمْ أَرْبَابًا مِّن دُونِ ٱللَّهِ وَٱلْمَسِيحَ ٱبْنَ مَرْيَمَ وَمَآ أُمِرُوٓا۟ إِلَّا لِيَعْبُدُوٓا۟ إِلَٰهًا وَٰحِدًا ۖ لَّآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ۚ سُبْحَٰنَهُۥ عَمَّا يُشْرِكُونَ

يُرِيدُونَ أَن يُطْفِـُٔوا۟ نُورَ ٱللَّهِ بِأَفْوَٰهِهِمْ وَيَأْبَى ٱللَّهُ إِلَّآ أَن يُتِمَّ نُورَهُۥ وَلَوْ كَرِهَ ٱلْكَٰفِرُونَ

Sun riƙi mãlamansu (da Shehunnansu (Yahũdu da Sufaye)) da ruhubãnãwansu (Nasãra) Ubannangiji, baicin Allah, kuma sun riƙi Masĩhu ɗan Maryama (haka). Kuma ba a umurce su ba fãce da su bautã wa

Ubangiji Guda. Bãbu abin bautãwa fãce Shi. TsarkinSa ya tabbata daga barin abin da suke yin shirki da shi.

Sunã nufin su bice hasken Allah da bãkunãnsu. Kuma Allah Yanã ki, fãce dai Ya cika haskenSa, kuma kõ da kãfirai sun ƙi. [Surah At-Tawbah: 31-32]

4.8 KAMMALAWA KAN SUFANCI

Sufaye suna rayawar Waliyai sunfi Annabawa Mursalai. Amma da fari menene ko waye Wali?

Wali shine duk wanda Allah ya ke so da fari, sannan shi kuma yake son Allah. Wannan shine Wali na haƙiƙa. Saboda haka duk Annabawa da Manzanni Waliyai ne. Walittakarsu ga Allah tafi walittakar kowa, domin saboda ƙaunar da Allah Ya ke musu, Ya zaɓe su da Annabta da Manzanci. Kuma su Shaida ta haƙiƙa ta zo akansu daga UbangijinSu cikin Littattafan da aka basu.

Amma a yanzu duk wanda kace Wali ne, to babu tabbas, kuma babu shaida ga da'awarka, sai dai kawai kyakkyawan fata. Idan kuma shi kansa ya faɗa cewar shi Wali ne, ina shaidar sa? Kuma waye ya shar'anta bin Wali ɗin da ka ce Waline? Mun sani Annabawa Manzanni, su Allah Ya ke aikowa domin shiryar da al'umma. Kuma Allah SWT Ya ce cikin Alƙur'ani mai Tsarki:

مَّا كَانَ مُحَمَّدٌ أَبَآ أَحَدٍ مِّن رِّجَالِكُمْ وَلَـٰكِن رَّسُولَ ٱللَّهِ وَخَاتَمَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ ۗ وَكَانَ ٱللَّهُ بِكُلِّ شَىْءٍ عَلِيمًا

FASSARA

Muhammadu bai kasance uban kõwa ba daga mazanku, kuma amma shĩ yã kasance **Manzon Allah kuma cikon Annabãwa**. Kuma Allah Ya kasance Masani ga kõme. [Surah Al-Aḥzāb: 40]

Kenan babu wani sauran ɗan aike da abin aiken. An gama ila yaumil ƙiyamati. Shi yasa Allah SWT Ya ƙarfafi wannan aya da:

حُرِّمَتۡ عَلَيۡكُمُ ٱلۡمَيۡتَةُ وَٱلدَّمُ وَلَحۡمُ ٱلۡخِنزِيرِ وَمَآ أُهِلَّ لِغَيۡرِ ٱللَّهِ بِهِۦ وَٱلۡمُنۡخَنِقَةُ وَٱلۡمَوۡقُوذَةُ وَٱلۡمُتَرَدِّيَةُ وَٱلنَّطِيحَةُ وَمَآ أَكَلَ ٱلسَّبُعُ إِلَّا مَا ذَكَّيۡتُمۡ وَمَا ذُبِحَ عَلَى ٱلنُّصُبِ وَأَن تَسۡتَقۡسِمُواْ بِٱلۡأَزۡلَٰمِۚ ذَٰلِكُمۡ فِسۡقٌۗ ٱلۡيَوۡمَ يَئِسَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِن دِينِكُمۡ فَلَا تَخۡشَوۡهُمۡ وَٱخۡشَوۡنِۚ ٱلۡيَوۡمَ أَكۡمَلۡتُ لَكُمۡ دِينَكُمۡ وَأَتۡمَمۡتُ عَلَيۡكُمۡ نِعۡمَتِي وَرَضِيتُ لَكُمُ ٱلۡإِسۡلَٰمَ دِينٗاۚ فَمَنِ ٱضۡطُرَّ فِي مَخۡمَصَةٍ غَيۡرَ مُتَجَانِفٖ لِّإِثۡمٖ فَإِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٞ

FASSARA

An haramta muku mũshe da jini da nãman alade da abin da aka ambaci sũnan wanin Allah a gare shi, da mãƙararriya da jefaffiya da mai gangarõwa da sõkakkiya, da abin da mãsu dãgi suka ci, fãce abin da kuka yanka, da abin da aka yanka a kan gunki (shĩ ma an haramta). Kuma kada ku yi rabo da kibiyoyi na cãca wannan fãsiƙanci ne, A yau waɗanda suka kãfirta sun yanke ƙauna daga addininku. Sabõda haka kada ku ji tsõronsu kuma ku ji tsõroNa. **A yau Nã kammalã muku addininku**, Kuma Nã cika ni'imaTa a kanku, Kuma Nã yarda da Musulunci ya zama addini a gare ku. To, wanda aka sanya wa lalũra a cikin yunwa mai tsanani, bã yana mai karkata zuwa ga wani zunubi ba, to, lalle ne Allah Mai gãfara ne, Mai jin ƙai. [Surah Al-Mā'idah: 3]

Kenan a cikin Musulunci babu sauran saƙo da za a aiko. An riga an gama ila yaumil ƙiyamati.

Saboda haka, idan a yau ka yarda da cewar, ga wani Wali ko Shehi, da ya ce Allah ko Annabi ya ba shi wani saƙo kan Addinin Musulunci, kuma ya umarci al'umma da aikatawa, to abu biyu ne yanzu a kanka, babu na uku;

1) Imma dai, waɗancan ayoyi ba ka san su ba, ko ka jahilci ma'anarsu.

2) Imma ka sansu kuma ka san ma'anarsu, kawai dai baka yarda da su ba, ko ka ƙaryata su.

Idan ka ƙaryata su ne, to ka zama kafiri da Nassin Alƙur'ani. Ga kuma abinda Allah SWT Ya ce ga kafirai ko waɗanne iri ne (na cikin gida da na waje):

أَفَحَسِبَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ أَن يَتَّخِذُواْ عِبَادِى مِن دُونِىٓ أَوۡلِيَآءَۚ إِنَّآ أَعۡتَدۡنَا جَهَنَّمَ لِلۡكَٰفِرِينَ نُزُلًا

قُلۡ هَلۡ نُنَبِّئُكُم بِٱلۡأَخۡسَرِينَ أَعۡمَٰلًا

ٱلَّذِينَ ضَلَّ سَعۡيُهُمۡ فِى ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا وَهُمۡ يَحۡسَبُونَ أَنَّهُمۡ يُحۡسِنُونَ صُنۡعًا

أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِـَٔايَٰتِ رَبِّهِمۡ وَلِقَآئِهِۦ فَحَبِطَتۡ أَعۡمَٰلُهُمۡ فَلَا نُقِيمُ لَهُمۡ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ وَزۡنًا

ذَٰلِكَ جَزَآؤُهُمۡ جَهَنَّمُ بِمَا كَفَرُواْ وَٱتَّخَذُوٓاْ ءَايَٰتِى وَرُسُلِى هُزُوًا

FASSARA

Shin fa, waɗanda suka kãfirta sun yi zaton (daidai ne) su riƙi waɗansu bãyĩNa, majiɓinta baici Na? Lalle ne, Mun yi tattalin Jahannama ta zama liyãfa ga kãfirai.

Ka ce: "Kõ mu gaya muku game da mafĩfita hasãra ga ayyuka?"

"Waɗanda aikinsu ya ɓace a cikin rãyuwar dũniya, alhãli kuwa sunã zaton lalle ne sũ, sunã kyautata, (abin da suke gani) aikin ƙwarai?"

Waɗancan ne waɗanda suka kãfirta da ãyõyin Ubangijinsu, da kuma haɗuwa da Shi, sai ayyukansu suka ɓãci. Sabõda haka bã zã Mu tsayar musu da awo ba a Rãnar Ƙiyãma.

Wancan ne sakamakonsu shĩ ne Jahannama, sabõda kãfircinsu, kuma suka riƙi ãyõyi Na da Manzanni Na abin izgili. [Surah Al-Kahf: 102 - 106]

A dunƙule:

Jalla Jalaluhu Ya ce:

وَمَنۡ أَضَلُّ مِمَّنِ ٱتَّبَعَ هَوَىٰهُ بِغَيۡرِ هُدٗى مِّنَ ٱللَّهِۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهۡدِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلظَّٰلِمِينَ

".....kuma wãne ne mafi ɓata daga wanda ya bi son zuciyarsa, bã tãre da wata shiriya daga Allah ba? Lalle ne, Allah bã ya shiryar da mutãne azzãlumai". Surah Al-Qaṣaṣ: 50

إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَغۡفِرُ أَن يُشۡرَكَ بِهِۦ وَيَغۡفِرُ مَا دُونَ ذَٰلِكَ لِمَن يَشَآءُۚ وَمَن يُشۡرِكۡ بِٱللَّهِ فَقَدِ ٱفۡتَرَىٰٓ إِثۡمًا عَظِيمًا

Lalle ne, Allah ba Ya gãfarta a yi shirki game da Shi, kuma Yana gãfarta abin da yake bãyan wannan ga wanda Yake so, kuma wanda ya yi shirki da Allah, to, lalle ne ya ƙirƙiri zunubi mai girma. [Surah An-Nisāʾ: 48]

إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَغۡفِرُ أَن يُشۡرَكَ بِهِۦ وَيَغۡفِرُ مَا دُونَ ذَٰلِكَ لِمَن يَشَآءُۚ وَمَن يُشۡرِكۡ بِٱللَّهِ فَقَدۡ ضَلَّ ضَلَٰلَۢا بَعِيدًا

Lalle ne, Allah ba Ya gãfarta a yi shirki da Shi, kuma Yana gãfarta abin da yake bãyan wannan, ga wanda Yake so. Kuma wanda ya yi shirki da Allah, to, lalle ne ya ɓace ɓata mai nĩsa. [Surah An-Nisāʾ: 116]

A yanzu haka an hana addinin Sufanci a ƙasar Turkiyya a Hukumance. Dalili kuwa shine Turkiyya ta ɗauki Addinin Musulunci shine Addinin ƙasar, kuma ta ce Sufanci ba Musulunci ne ba.

Haka abin ya ke a Alƙahira, koda yake takunkumi aka sanya musu kawai a can.

Ya Allah muna roƙonKa kariya da mu da zurriyarmu daga taɓewa cikin Addini. Duba Littafina mai suna "Matsalolin Musulmai a Junansu".

5. SAKAMAKON ABINDA SUFANCI YA HAIFAR A TSAKANIN MUSULMAI.

Sufaye, Tijjani, Inyass da Tijjaniya sun ZALUNCI Musulman Africa - Africa ta Arewa, Africa ta Tsakiya da Africa ta Yamma. Sun haifar musu da sabon Addini cikin Addinin Musulunci ta yadda suka bar muridansu cikin baƙin Jahilci. Ba ruwansu da neman haƙiƙanin Ilimin Alƙur'ani bisa koyarwar Fiyayyen Halitta Muhammad ɗan Abdullahi Balarabe farin Jakada SAW.

Saboda an saukar musu, saukarwa ta ƙarya, da wani salati wanda suka ce "ladan karantashi sau ɗaya, yafi ladan karance Alƙur'ani sau dubu shida". Duk wanda ya yarda da wannan, yaushe zai ɓata lokacin sa, wajen karatun Alƙur'ani har ya fahimci ma'anoninsa ya yi aiki da shi? Allah Ya isa.

Musulunci ya koyar da Tauhidi tsantsa (Allah Shi kaɗai ne Abin Bauta, kuma kowa Bawa ne). Sannan Musulunci ya koyar cewar Manzon Allah SAW shi kaɗai kawai, za a yiwa biyayya wajen koyon yadda za a yi wannan Bautar. Sannan Annabi Muhammad shine Manzon ƙarshe, kenan babu wani sabon abu da za a aiko har Ranar Busar Ƙaho. Duk wannan Sufaye sun ƙaryata.

Saboda haka, sai ya kasance dukkan ɗariƙu, da na Sufaye da ba na Sufaye ba, saɓanin haka suke koyarwa. Sun haddasa jahilci da gaba tsakanin Al'ummar Manzon Allah SAW.

Wai yau, mai kira da a kaɗaita Allah da Ibada (Tauhidi), a kaɗaita Manzon Allah SAW da biyayya, wai su ake cewa maƙiyan Manzon Allah SAW. Wannan wanne irin ruɗu ne cikin Addinin Musulunci?

Ya Allah Ka kawo mana mafita. Ka ɗaukaka Musulunci da duk waɗanda suke kira ga hanyarKa ta daidai, Ka ƙaskantar da duk waɗanda suke kira ga tafarkin ɓata, tafarkin Shaiɗan la'ananne. Aamiiin Ya Rabbal 'Alamiin.

6. INA MUKA DOSA?

Tabbas ko shakka babu kowa ya san mun doshi wani guri. Gurin da hanyarsa ta kasu gida biyu, hanya mai kyau, amintacciya da rabauta, da kuma ɗaya hanyar mummuna, wadda ba tabbas, ta halaka da taɓewa.

Kowannenmu yasan wata rana zai bar duniyar nan, zai koma ga Mahaliccinsa, watau Allah SWT. Kuma dole takan ɗaya daga cikin hanyoyin can zai bi. Alagafarta Malam, wacce ka zaɓa daga ciki?

Hanyar Annabawa da Manzanni na haƙiƙa kamar Hanyar Manzon Allah SAW, wadda take kyakkyawa tabbatacciya mai Aminci, ko hanyar Sufaye maras tabbas masu bin Waliyai na ƙarya da Shehunnai na bogi zuga ga molon ka da Shirka da Zindiƙanci da taɓewa?

Saboda haka zaɓi ya rage gareka! Babu mai matsa maka, domin Allah SWT Ya baka hankalin da zaka iya rarrabe tsakanin mai kyau da maras kyau, sannan cikin IkonSa da HikimarSa da ƘaddararSa, Ya bar maka ikon zaɓi. Sannan Ya ce Zal Jalali wal Ikraam:

فَمَن يَعْمَلْ مِثْقَالَ ذَرَّةٍ خَيْرًا يَرَهُ
وَمَن يَعْمَلْ مِثْقَالَ ذَرَّةٍ شَرًّا يَرَهُ

FASSARA

"To, wanda ya aikata (wani aiki) gwargwadon nauyin zarra, na alheri, zai gan shi".

"Kuma wanda ya aikata gwargwadon nauyin zarra na sharri, zai gan shi".
[Surah Az-Zalzalah: 7 -8]

A ƙarshe, Hukuma idan ta Musulunci ce, kamar a nan Kano, wajibi ne ta karewa Musulman Kano Addininsu ta hanyar Tsabtace shi daga dukkan wata kwamacala ta yan Bidi'a da Sufaye da Yan Tatsine. Addinin Musulunci

Addini ne ƙwaya ɗaya tak, kamar yadda muka gani nan sama. Duk wanda ya ƙirƙirar da wani abu, kuma yayi cushensa cikin Musulunci, to shine da kawo dalili. Idan ya kasa, dole Hukuma ta DAKATAR DA SHI. Idan ba ta yi ba, zata zama abin tuhuma da zargi da samun mummunan sakamako daga Rabbul Izzati Ranar da wata rai ba ta amfanawa wata rai da komai, sai wanda ya jewa Allah da zuciya kuɓutacciya (daga kowanne zargi).

Hadith (Kullukum Raa'in wa Kullukum mas'u.....)

Tammat.

Ya Allah Ka ƙara daɗin Tsira da Aminci ga Annabin Rahama Muhammad SAW, da Iyalan Gidansa Tsarkaka da Sahabbansa Adalai masu daraja da ragowar Muminai da su ke kan tafarkin Manzo har Ranar Ƙarshe.

Bldr. Ibrahim Muhammad Dankyauri, Jumada ula 1447 AH / October 2025

Takaitaccen Tarihin Marubucin Littafin.

An haife ni wajejen shekara ta 1959/60 Miladiyya (a kan takardu 01 July 1959), a zahiri, (Friday 02 Oct. 1959 kamar yadda Mahaifiyata ta faɗa mini cewar an yi husufin rana cikakke a ranar da ta haifeni wanda ya dace da wannan kwanan watan), a can Garin Garko cikin ƙaramar hukumar Garko, jihar Kano, Nijeria. Kuma nayi karatun primary a Garko central primary daga 1966 zuwa 1972. Daga nan na tafi secodary ta Birnin Kudu a shekara ta 1973 zuwa 1977. Na fara college of Advance Studies CAS Kano a shekara ta 1978 amma saina sami tafiya ƙasar France domin karatu cikin shirye shiryen Crash Programme lokacin gwamnatin soji ta Obasanjo. Na karanci Building Construction (Injiniyan gine-gine da sarrafa fasalin doron ƙasa). A can France na yi karatu cikin wasu makarantun dake garuruwan Toulouse, Lyon da Caen. Na dawo nan Nijeriya bayan nayi shekara shidda a France, cikin shekara ta 1984, da takardar shaidar karatu kwatankwacin HND ta Nijeria akan fannin karatun da nayi (Brevet de Technicien Supérieurs (BTS), Adjoint Technique d'Entprise du Bâtiment (ATEB)). Kuma nayi NYSC a tsohuwar Gongola state a shekara ta 1984/85. Nayi aiki a kamfanoni da yawa (Nigeria Roads Construction NRC, Kabo Holdings, Nigeria Engineering Construction Company NECCO da sauransu), da kuma cikin gwamnati (SUBEB Kano, STSB Kano, Nigeria Directorate for Employment NDE da sauransu), . Na ƙara karatu kan "Civil Engineering Structures zuwa matakin PGD. Na fara karatun Masters a wannan fanni amma banyi "coping" da "Nigeria's factor on Education", sai na bar wannan karatun. Na yi register da "Nigeria Institute of Building" (NIOB) da " Council for Registered Builders of Nigeria" (CORBON) wadda a yanzun nan Ni "Registered Builder (Bldr.)" ne. Na yi "retire" tuni daga aikin Gwamnati. Kuma dai tuni nayi aure da ƴaƴa har da jikoki. Alhamdu lilLahi.

Lokacin da na dawo daga France, bayan na gama NYSC 1984/85, sai kawai naji lallai ina da buƙatar ƙara sanin Addinin nan nawa, saboda haka na shiga makarantar dare ta manya a can makarantar Dakta Aminuddeen

Abubakar (Allah Ya jiƙansa da Rahama) a sulaiman crescent Kano, Shekara huɗu zuwa biyar nayi anan. Haƙiƙa ba ƙaramin ƙaruwa nayi ba a wannan makaranta domin daga nanne na sami kwaɗayin zuwa gurin karatuttuka daban daban da nufin ƙarin ilimi. A waccan makaranta ce dai na fara iya rabe tsakanin ء da ع tsakanin ص da س da ث da kuma tsakanin ض da ظ da ذ da ز da kuma tsakanin ح da ه cikin lafazi da kuma hukunce hukuncen karatun Alƙur'ani wato Makhaarijul Huruuf da Tajwidi, da dai sauran fannoni na ilimi, kamar Tauhidi, Fiqhu, Sirah. Sannan na daɗa shiga makarantar koyon Larabci da Addinin Musulunci ta Alfurƙan dake Ɗorayi, nan kuma shekara biyu, inda na samu "basic" cikin Nahwu, Sarf, Balaga, Tafsir, Tarikh da sauransu. Haka kuma dai, ba ƙaramin ƙaruwa nayi ba wajen halartar karatuttukan su Dakta Ahmad Ibrahim Bamba a can masallacin BUK wato Darul Hadith da Gadon ƙaya wato masallacin Sheik Malam Ja'afar duk a nan Kano, da kuma sauran gurare masu yawa. Alhamdu lillah, Allah Ya sakawa waɗannan manyan malamai namu da mafificin alherinSa duniya da Lahira. Amiin. Jama'a, a cire ƙiwa a tashi a nemi Ilimi akwai aiki a gabanmu, domin kuma dai ba a girma da neman Ilimi. Alhamdu lilLahi. Bissalaam.

Intentionally left blank